Copied By
HAYATU BABA ZUBAIRU
(admin
Arewa hausa novels
Novels villa
Duniyan novels
Hayat hausa novels
Hausa novels and fashion
And
Cool novel, makeup and cooking)

WHATSAPP NO:
+2347039625239
[2/18, 10:36 AM] +234 703 962 5239: 25/10, 5:10PM
♡DUTSEN CIKIN RUWA.....♡

GARGADI:banyarda wani ko Wata yajuya min min wannan kirkirarren labari nawa ba,banyi Dan wani ko Dan Wata ba,sunayen da garuruwa naciki da nasa dukdan su nishadantar dame karatune banyin dancin fuskaba saboda haka kada ajuyamin wani sashe ko wani bangare naciki batare da izinina ba inhar hakan tafaru NAJA ALLAH YA ISA!!!!

..♡..♡..♡

STORY AND WRITTEN BY:
HALEEMA G KHALEEL

01

Cikin sauri-sauri take tafiya kada lecturer insu yarigata shiga, sabida dokarshi ce inyarigaka shiga tom sede katara next,time.
Dauke take da lab-cout da sch bag inta dressing inta wanda kusan kullum shine shiganta, gown ne eather Material, Atamfa, ko Ready made kiran Bahrain Oman, ko Kuwait.
Yanxunma Gown ce jikinta Sea,green tayane kanta da peach colour veil. Kannan yasha Top-knot. Setashin sanyin kamshi take, wanda bazaka tantance wana irin perfumes take using ba.
Akan kwanan dazata sadata da Biology Lab insu tagansu sunata K'us-K'us i. Tai saurin fadin " ````LA ILA HA ILLA ANTA SUBHANAKA INNI KUNTU MINAZ ZALIMIN```."

Inda sabo tasaba dahakan dasuke mata koyaya zata hadu dasu sesunyi magananta. That Y! tabama "Innansu labari tace mata tai ta addua duk wani mai nufinta da sharri, in sha Allah baze tasiri a kantaba.
Musamman yadda bata shiga abinda bishafeta tun a farkon zuwansu sch in, duk abinda baruwanta bata minding buissnes inta akai. Hasalima bata fiya maganaba bakowa take kulawaba. Hakan yasa dayawa dakacin mates innasu suke ganin girman kai gareta especially Shema da Zuzu. Tun farin karatunsu suke shigemata datagan ba karatunne gabansuba yasa ta

ajesu a Side. Hakan yasa suke takun saqa dasu.. A bakin kofan Lab in tatsaya tasaka lab-court inta tana zura Tag inta agaban rigan taji anbangajeta.

Tag in yai gefe tai taga2 zata fad'i tai saurin dafa jikin block in. Ko ba a gayamataba tasan bazasu wuce Shema da Zuzuba.

Daukan Tag inta tai tasa tashige Lab in batareda ta dubi kowaye yamata hakaba. Tareda qudurcewa a ranta matuk'ar yau aka had'asu Group daya a Practical in bazata shigaba sede yakoreta.

Yanadaka gefe yagan duk abinda yafaru yaji tak'ara birgeshi matuk'a shima yarufamasu baya yashiga Lab in anata hayaniya seda practical teacher in yaxo kowa yanutsu. Yai dividing insu Group Group. Allah yataimata group insu daban2, su biyu mata daka ita se Jidda ja'o. Aka fara practical in Tissue Respiration. Tanata hadamasu Apparatus tazo aje ruwa kawai tazubama USMAN BELLO GALADIMA ajikinshi. Gashi dama yabi yasa mata idanu duk abinda take idansa nakanta tun shigowanta dasafe.....

To suwaye wadannan??
Kutara kusha labari

IN DEDICATION TO MY ANEE AND MISS XOXO......
✍
ANISA_DIDI🍼🍉😜
[2/18, 10:37 AM] +234 703 962 5239: 26/10, 9:30AM
♡DUTSEN CIKIN RUWA.....♡
Na
Haleema G Khaleel

Godiya ga Allah. Godiya agareki ANTY AZIZA I GOMBE{```UMMYASMEEN```} Allah yabar k'auna❤

02

A haka har suka kammala practical innasu duk da ita atakure take yadda yaketa satar kallanta.. Kiran Attendance malamin yayi kowa yai ficewarsa.   Har suka kammala darusan ranar.

Agajiye liss tada gida kayanta kawai ta ajiye tashiga band'aki, wanka tai tareda d'auro Alwala. Shiryawa tai tanufi d'akin Innarsu.
Zaune tasami Innar tana ta gyaran kayan K'annanta, gefanta kuma Ahmad(deedat) dan,autansu yanata rikici Inna tahanashi fita. sannu da gida inna tafada cikeda ladabi, Innan ta amsa fuska sake. To Rigimau miye kuma? NAJA'ATU tafad'a tareda janyoshi jikinta. Meya faru da d'an Inna? Tace masa tana shafa kansa, alamun rarrashi. Ba Innace tahanani futaba, yafad'a tareda

rufe idansa waishi yayi fushi.

Haba Deedat banda abunka ai Inna tayi dai-dai datak'i bari ka futa bakaga Magriba takusaba. Kuma ba asan Yawo, yahakuri kaji wataran zamuje unguwa muma ko? Damurna ya amsa yace ah! Har gidansu Anwar zaki kaini muhau lilo ko? Yafara tsalle yana murna yasaki ransa kaman bashiba.

Murmushi tai k'asa-k'asa takallo Innar tasu da itama Deedat in yasata dariya. Naja'atu tace Inna gara shima Deedat asashi a Makaranta tunda ankusa d'iban sababbin D'alibai. Wannan surutun da san yawan nasa duk ya ragesu.

Ajiyar zuciya Innar tayi hmmm! Yayar,Salim kenan. Domin Innar bata fa'dar sunanta itace 'yarta tafari. Su zauna si hirama seda Najar ta dage. Dan ita Innarsu Al-kunya gareta irin na iyayen daa. Kuma inbatai da itaba dawa zatayi tinda Rayuwar tazama Naka sai naka. Dadin zama sai bare inji Hausawa.
Innar tace Allah yakaimu muga yadda za'ayi. Domin Rayuwar gidannan tana bani tsoro. Hakuri zamu kara Inna, wataran sai labari Naja'atu tace tana mai share hawayenta.

Mutara domin jin gundarin labarin!!!

Didi_Aneesa🍼🍉😜
[2/18, 10:37 AM] +234 703 962 5239: 28/10, 5:07PM
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*.....♡
Na
*Haleema G Khaleel*

Godiya sosai *ummyasmeen*. Allah bar kauna❤

WAIWAYE:

0️⃣3️⃣

Alh,Abdul mu'iz Auwal Getso shine Mahaifinsu Asalinsa 'yan Getso ne dake Gwarzo, su uku mahaifiyarsu Iya Rakiya tahaifa Baba,Barira seshi Abdul Mu'iz da k'aninsa Muhammadu.

Dakanan kuma Allah yakar6i abarsa, hakan yasa mahaifinsu k'arin aure. Ya auri Baba Asabe. Har itama tahaifi nata 'ya'yan su biyar hudu mata d'aya Namiji Azeema, Furera, Saudat, Kareema sekuma Umar autansu..
Rayuwa sukai cikeda k'aunar junansu, suntaso duka kansu a had'e. Baba Asabe takula dasu dukansu. Bata yadda wani zaije gidan yaga Alamun ba ita tahaifesuba. Sunsami tarbiya da karatun addini dana zamani dai-dai misali. Har yasamu yashiga F.C.E Bichi ita kuma Barira aka mata Aure.. Haka har lokacin da kowannensu yai aure. " Ta dalilin cigaba da karatunsa

yamaidahi Birni". Yafara kasuwanci. "Tinda 6angararen dayake kenan".

Yana zaune a unguwar 'Dorayi,Babba. Ba laifi yayi Aure-Aure.

"Hajiya Aina'u itace matarsa ta lalle. Tanada 'ya'ya biyar. Tarasu awurin haihuwarta ta k'arshe. Matarsa ta biyu kuwa. ```Auren,zuminci```, akaimasu da ita wato Mama-Lubabatu itama 'ya'yanta takwas dashi.

Dakanan ya Auri Momy Lami da Goggo Safiya. Goggo Safiya itama 'ya'ya takwas ta haifa.

Tarasu yai su duka "yasanar masu zai 'kara Aure". Bakowo bace kuma face, Ummu-Salma. K'anwa gawani abokin cinikayyarsa dake Gusau. "Wadda itace Innarsu Naja'atu".

Jin hakan bak'aramin Tayarwa da Momy Lami hankali yaiba. Ta tada K'ayar baya. "Hakan kuwa yai sanadiyar barinta gidan.

Inna Salma itace matar daya auro ta 'karshe kuma yake Matuk'ar santa da tausayinta. "Domin tasha wahala agurin mutan gidan dama 'ya'yansa mata manya dasuke ganin Sa'arsu aka auro." Kuma tanama kansha.

Danma tana Hak'uri da kawar dakai gameda abubuwa da dama.

**********

Wannan kenan!!!

*Didi_Aneesa*🍼🍉😜

[2/18, 10:40 AM] +234 703 962 5239: 29/10, 12:30PM

♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*....♡

*Na*

*Haleema G Khaleel*

0️⃣4️⃣

Banafsha itace Babbar 'ya agidan, Allah yayita mai Larurar, Kurmanta dakabaya ma ta,rasu. Daka ita sai Habiba, se yaya Lawan shine babban namiji kuma 'da na uku duk 'ya'yan hajiya Aina'u ne takuma haihuwar Adam inda A haihuwar Kausar ta rasu. Se rik'onta yakoma gurin Mama Luba. Itama 'ya'yanta takwas. Dina, Fadil, Bahijja, Fahad, Haris, Labiba, Rumaisa da Habibu.

Momy Hadiza kuwa 'ya'yanta hudu: Bilkisu, Afiya, Fa'iza se Musa su kadai tahaifa tabar gidan. Inda Goggo Safiya takeda Takwas itama: Hafiz, Idrisa, Mabruka, Madina Bilal, Dauda, Nasir da Juwaira.

. Inna Salma, Mahaifiyar su Naja'atu. Tun lokacin datazo gidan, Dina da Habiba sunga Sa'arsu mahaifinsu ya auro suke taya Iyayensu Kishi. Bak'aramin wuya tasha agurinsuba. Gashi bata haihu da wuriba sedaka baya. "Bayan anmasu Aure har Dina tahaihu" da shekara biyu sannan Inna Salma tahaifi tagwaye, Isma'il da Ibrahim. Sannanne haihuwa ta bud'e mata akai-akai.

"Ta haifi  Naja'atu dak'annanta Kamal, Samiha, Fawad , Salim da Autansu kuma Autan gidan, wato Ahmad(Deedat)".

Duka 'ya'yan gidan su 32 ne biyu sun mutu.
Naja'atu itace 'ya ta Ashirin da biyar Agidan. Duka in an ha'da da kannanta tara dana sauran d'akin dakuma wadda suke Uwa daya Uba 'daya.
"Alh Abdul-Mu'iz yakasance mai yalwatawa iyalansa komi dayake ahakkun Uba shiyakeyi. Makaranta mekyau da tarbiya gwargwadan iyawarsa " Lokacin dayake kan samunsa. "Tinkamin karayan arziki tasameshi.

Watarana Inna suka tashi Samiha bata da lafiya, ciwan ido dakyar aka wanke, mata da ruwan 'dumi yabud'u.
"Ga Alh, bashida kudi"
Sukarasa yazasiyi,
Ita ba sana'a ba.

dakyar Hafiz d'an Goggo Safiya yasamo mata 'dari hu'du. "Dominshi yana tausayamata" kuma jininsu ya had'u. "Tamaidashi tamkar ita ta haifeshi ita dama bame zafi ba".
Sau dayawama inyasamo 'yan ku'di wurin sana'arsa yakan raba biyi yabata, duk abinda yasameshi kuwa na dad'i ko akasin haka zai gaya mata tabashi shawarwari. Kuma yaga fa'idan hakan.

Hausawa sukace ```Abinda babba ya hango, yaro ko yahau Dala baze ganoba.```

*Aneesa_didi*🍼🍉😜
Anisadidi.pun.bz
[2/18, 10:40 AM] +234 703 962 5239: 30/10, 4:17PM
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA* ♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

0️⃣5️⃣

Da d'ari-hudu da hamsin, tahad'a suka tafi Asibitin, Murtala dake cikin gari,
Dukda haka bak'aramar tafiya tashaba, duk dan tarage kudim motan.
Aka duba Samihan aka bata magani. Sunsha wiya kafin sudawo.

Da dawowarta tatarar da abin mamaki. "K'aninta Sa'ud yazo daka Gusau" . Da farincikinta tatareshi. Dukda bata da wani abu dazata bashi. Koba komi ```Shinfidar fuska....  Tafi ta tabarma```.

Balle d'an uwanta dasuke ciki d'aya dashi.

Sannu da zuwa sukaima juna. Yakarb'i katin asibitin, segani tai yafuta.
Tare dasu Isma'il suka shigo, yasiyo mata magungunan da madara me sanyi.
Bayan ya huta yaci yasha.
Yacikasu da tsaraba da Mahaifiyarta tahad'o yakamata, kwana2 yai yacikasu da shatara ta Arzik'i. Yakoma Gusau.

Haka rayuwa taita tafiya, Inna nacigaba da fuskantar k'alubalen rayuwar gidan iri-iri, da dad'i ba dad'i. Tana cigaba da hak'uri. Sabida 'ya'yanta " sune k'ananu agidan, kuma sune abun a tausaya musu. Naja'atu da yarinta, tin bata fuskantar abunda akema Mahaifiyarsu harta fara ganewa.
Dukda tataso cikin gidan yawa.
Allah beyita mai hayaniyaba, asalima batada yawan magana. Hakan datakeyi yasa wasu daka cikin yayyunta mata kecemata "Munafuka. Sumimi kasam. Kawai saidai tai murmushi. Inta gayawa Innarsu tace mata tayi hakuri, 'yan uwantanw." Wataran zasu dena.

*bayan shekara5*
*Cigaban-labari*
Naja'atu yarinyace mai sanyin hali. Duk wasu haleyenta nak'warai tasamosu daka Innarsu.
Kyakyawace sosai, farin dangin babansu kawai ta d'akko, hatta yatsunta da sirantarta, na Innane asalinsu fulanin Gusau ne. Akwai dukiyar fulanin. Sedai batada tsayi sosai.
Tashare siraren hawayenta. Tana tunanin wannan rayuwa. Wani abubuwanma sabida ganin idon Babannasu ake bari. To inaga yafad'i yamutu! Yazasiyi?
Taja nannauyar ajiyar zuciya. Hmmm!!

*Didi_Aneesa*🍼🍉😜
Anisadidi.pun.bz
[2/18, 10:41 AM] +234 703 962 5239: 31/10, 5:15PM
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*♡
*Na*
*Haleema G khaleel*

06-10

Ranar takama lahadi. Bata da sch, bayan ta kammala gyaran dakin Innar tasu, tashare tai moping, se tashin k'amshi dakin yake bakace sunada masu fitsarin-kwanceba.
Babban floor ne se dakuna guda biyu da band'aki. Da k'aramin kitchen agefe. Inna da Samiha da ita, a d'aki daya, "d'aya kuma kananun k'annanta mazane su3 ne aciki.

K'a'idar Alh ce dazarar yaro namiji yakai shekara 10 -12 za a maidaka waje boys quaters, haka duk sauran d'akunan matan gidan yake. Dukda akwai babban Kitchen, wadda takeda girki ita zatai azubama kowane 6angare.

Misalin 10am Hantsi yad'aga, tayi wankanta tanata tashin k'amshi, gefanta ☕ruwan-bunune, da

wainar gero taji k'uli😋. Tagama karin safenta, tahau yin tsifa. Tawanke kan, ta gyarashi. Dan dama ita ba ma'abociyan san kitso bace, duk da yawan gashin datake dashi.

Kitchen tashiga. Dan taya Innarsu had'a abincin Rana. " Tuwan dawa, da miyar d'anyar kub'ewa taji busashshen kifi. sukayi. Suka kammala. Takaima kowana d'aki nasu. Sannan takimtsa gurin.

Dakomawarta d'aki sallah tai, ta d'an shingid'a, Nannauyan bacci yai gaba da ita. K'arar wayanta ne yata data. Hafsa Hussain ce, 'yar ajinsu a islamiyya.

"Salamu Alaikum ukty"

Daka d'aya 6angaren Hafsa ta amsa, suka gaisa hafsa tak'ara mata tunida Aikin da aka basu cikin littafin ``` *Durusulluggatul arabiyya* ```domin tayi kada tazo a hukuntata cikin wanda basiba. Tad'anyi mata bayani darasun dayadda zatayi. "Sukai sallama. Sesun hadu a islamiyyan. Duk da bakullum take zuwa ba. Amma tana kiyaye kowane abu dazesa a hukuntata.

Sauri tai tad'akko jakanta, tafara yin aikin, tai iya wanda tagane, sauran kuma in sunje Islamiyyan kan akar6a takarasa.

Wanka tafarama Salim shi kuma Kamal yai nasa suka shirya seda suka jira Samiha ita ma tashirya sannan

Naja'atu tasasu agaba sukama Inna sallama 3:30 suka tafi a hanyar islamiyyan, suka hadu da Fawad yayi futu-futu da alama daka fillin ball suke. Salim yace" yaya,Fawad yau bazaka makarantaba? "Ganin kallan da Naja'atu kemasa ya hau sosa k'eya. Yanzun zan shiryo nataho. Yafiye maka de tafad'a. Danshi tin yana yaro inda abinda yafi tsana to ace yatafi makaranta. Tin ana dukansa har akagaji aka basshi. Kunsandw maza dak'in makaranta.

Musamman Islamiyya. Sukai gaba suka barshi karya sasu latti.

Bayan an idar da Sallah, kowa yai Ajinsu.

A Ajin su Naja'atu maza sun zauna matan ko suna tsaye basu sami Tabarma ba, gashi indai Malam yariga yashigo sede su zauna ak'asa.

Yadda kua sukeji da gayu,😉(miss u gayu-gayu). Nafisa tatashi sarkin tsiwa😜 aiko tama mazan tatas hadda fad'in basa kishinsu. "Su sunsamo abun zama amma su ko oho. Wani dan ajin Sanusi yaita bata hak'uri. Yafita yasamo masu.

Hannun Naja'atu taja dukda ita bame yawan maganabace, se ma abum yabata dariya ganin anja Hafsa,Sady da Nafisa hassan. Aji-Aji sukai tabi, Har suka gano Tabarmassu.

Aikan ansha jaraba kafin su kar6o. Wata Fiddausi a ajin ta tashi tanata sirfa masifa, sega Malaminsu Malam,Farouk, yakirasu shima yahau nasa waisu sun had'e kai farare, se rashinji sukai. Nafisa kuwa ta Cuno baki😚(mom heena😂).

Yace "kuma karna k'ara ganinku haka batare da kunsa bak'a acikinkuba. Amsawa sukai yace kowa yakoma Ajinsu.

Nafisa sarkin mita kuwa tai tayi d'ayan Nafisa da Sady natayata. Sukuwa Hafsa da Najah sede si murmushi.

Akasa tabarma kowa yazauna. Suka kara jerewa su biyar a layi. Ita Naja'atu sarkin tsoro k'ok'arin chanja waje take aikua Nafisa tajawota hartana k'okarin fad'uwa abinka da ba k'iba.

Muraja'ar Al-qur'an akafara. Hakan yasa kowa ya nutsu.
Sukai karatunsu suka gama. Har aka kammala karatun. Malamin Arabiyya yaxo ya ansa Aikinsa dukda bata gamaba, haka tabayar..
"K'arar K'ararrawace ta ankarar dasu. Sunata surutu. Sukai addu'a kowa yatafi.
Abakin get in Makaranta ta tsaya jiransu Samiha, suka rankaya sukai hanyar gida. "Kamal bazaka tafi a hankali ba! "Kullum kai kenan kaita gudu ahanya sekace yaro. Bakaganin ko Salim baya abunda kake."

Bata ankaraba sejitai Kiiiiiiiy. Mota tai gaba da Kamal...
Waiyoo yaya kamal Salim yafad'a da k'arfi. Ita kua Naja'atu tama rasa mizatai. Se hawaye Shaar😥. Saurin Tarota Samiha tai ganin tana neman fad'uwa.
Innalillahi kawai taaji ana furtawa😳

Kubiyo didi👉🏽

*Aneesa_didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:41 AM] +234 703 962 5239: 1/11, 12:18PM
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA* ♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

1️⃣1️⃣-1️⃣2️⃣
Jitai itama ta fara maimaita ```Innalillahi wa inna ilaihi raji'un```. Bold eyes inta takuma zarowa😳.
Sukai saurin k'arasawa inda Kamal yake a yashe, Samiha ce tai k'okarin d'agashi. Razanannen Ihun da Kamal in yasa, bashiri Samiha ta sakeshi.
Naja'atu tace Kamal sannu kullum gayama nake kadena gudu amma kak'iji ai kaga irinta. "Kuka yafara yana waiyo Allah yaya k'afata waiyo Inna.
Shikuwa wanda yakad'eshi da motan,
*mukhtar* ne. Anan unguwar suke.
D'ane ga Alh Mahmud Ateeku. Da matarsa Haj Uwani, sun haifi, Mustapha, Zainab se Mukhtar Shine d'a na uku agidansu, da k'annansa Leena, Ummi da Iman autarsu.
Mukhtar kyakyawane, kamar shiyai kansa sede bak'i ne shi domin 6angaren mahaifiyarsa dake kathoun a Sudan yayi.
Dan wasuma Bak'in-Balarabe suke kiransa a family. Sede yakasance gagararren Yaro ne, duk irin yadda Iyayen nasu suka jajirce akan tarbiyassu. Amma abin nasa k'aruwa yake. Sabida muggan abokai daya had'u dasu. Gangs guda garesu. Na 'ya'yan masu hannu da shuni.
Shaye-shaye suke kamar ba gobe. Kotayaya kuwa se annemo kayan maye. Bawanda besansuba. Musamman M.M Ateek dawani Shanto. Shikuwa Maude 'yan zugane. Tinda iyayensa bamasu kud'i bane. Yawanci kullum suna hanyar Gwazaye. Ko kamasu akai yasan abokan zasi belinsa. Shiyasa yake biye masu.

Ganin haka se suka yanke shawaran akaishii karatu Dubai. Duk dan arabashi da abokanansa na nan dasuke k'ara janshi cikin sharholiyar rayuwa. Aikam bata chanja zaniba. Sema Wak'a dayaje ya koyo.

Sau biyu Alh M Ateek yana kaishi gidan mari, dan yasamu Horo yabar shaye-shaye dayakeyi.

Bayan anfito dashi akaro na biyu. Se sukadena bashi kudi akai-akai.
Yakoma indai zaiga kud'i saiya d'auka, kowani abu dazaika kudi' tokuwa zai d'auka su siyar da abokanansa. Kawai suse kayan maye.

Yanzunma Motar gidan yad'akko ba asaniba, tunda ko mota andena barinshi yahau shi kad'ai..

Yanata Falla gudu, aikam yabige Kamal. Futowa sukai shida abokinsa Wizzy, Mukhtar kuwa yahau Masifa "kawai yara ansakeku a hanya kaman dabbobi. Bakusan me kukeba. Yanzun ni gashinan anjamin 6ata lolacina, a wofi" yanata sababi.
Calm down abokina, wixxy yafurta hakan. Suka k'arasa gurin, Samiha kuwa mizatai inba Harararsuba. "Kobakada ido ai se haka malam har dazakana had'a mutane da dabba, sabida bakasan darajar mutaneba" dantasan im Naja ce bazata ce komiba.

Shikuwa Mukhtar Mamakine yacikashi. Wannan 'yar yarinyar dabatafi sa'ar Ummi k'anwarshiba take gayamasa magana.
Gani sukai yayyansu biyu sunzo ya, Hafiz da Isma'il. Domin sunkusa kaiwa gida. Salim yaruga yafad'a agida.
D'aga Kamal in sukai subiyi, yasami gocewar kashi a k'afarsa gashi duk ya kukkuje. Ganin hakan yasa Mukhtar in cewa susashi a motar. Suka tafi kaishi, Asibiti.

Ita kuwa Naja'atu k'wak'k'waran motsi kasawa tai, se Hawaye dake tabin fuskarta😪
Ahaka suka k'arasa gidan. Samiha kua se mita take. Dashigarsu Mutan gidan wasu na tsakar gidan sukaimasu jaje da Allah yakiyaye. Masu jaraba kuma, suna tayi. Itadai sum-sum tashige d'aki.

Tanaji samiha tanata maidama da Inna yadda akai, da mita akan sanyin yayartasu, abin yai yawa. Wataran ma ko taresu akai za amasu duka ita sedai tai. Shiru.
Murmushi Innar tayi. Tace bakomi daka Allah ne. Ai "kema Samiha kidinga hakuri kina rage fad'a da maganannan taki."
Ai shikenan Inna, Allah yak'ara kiyayemu, tai band'aki abinta.

Bayan magriba, sukaga shiru, basu dawoba. Itadai duk jikinta yai sanyi. Tahau bama Inna hak'uri, "Wallahi Inna Kullum anatafiya shi baze tsayaba sede yaita gudu. To yau tsautsayi se wani d'an unguwannan yabigeshi."
Bakomi ai Yayar-Salim Innar tafad'i. Tareda Addu'ar Allah yamasu Albarka yak'ara kiyayewa.

Suma su kuma kulawa dakansu suduka...

Allah kakara tsaremu Ameen!!!😄

*Aneesa_didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:41 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

1️⃣3️⃣-1️⃣4️⃣
Su yaya,Hafeez da Isma'il kuwa basu suka daba se wajen 9:PM.
Shikuwa kamal Annad'e inda yasamu gocewar, da dressing inda yajijji ciwo. Kwantar dashi sukai  d'akin inna. "Ga kayan mak'ulashe da MM Ateeqs yasiyamai, daya saukesu yak'arasa gida".
Itakuwa Naja'atu d'aya  d'akin inda su Saleem da Deedat suke can takoma tai kwanciyarta. Tabarma Kamal sukwana tareda Inna da Samiha, akan gadon.

Shikuwa Mukhtar, duk irin abubuwan dasuka dad'e suna aikatawa, Yau kad'ai yafarajin badad'i abinda yake, yafara tunanin yadda yarinya k'arama zata tsaya tana mayar masa da magana, kuma yakasa d'aukan Action akanta. Duk rashin Mutuncin dayakema 'yan matan dasuke nemansa. Baya biye masu. Duk iskancinsa baya neman mata, abarshi da shaye-shayensa,na syrup tabama se ransa yai mugun b'aci zeta busawa. Yanzun gashi ga Taba amma yakasa busata.
Jiyake inama yazama Mutum cikakke, yadda ba mahaluk'in dazai kamasa Raini.

Rana ta farko da Mukhtar yaji Nadama tafara shigarsa. Kallan kansa yatsayayi a madubi, meya nema yarasa? Dazai jefa rayuwarsa cikin wannan hali! Harhada duk wasu tarkacen kwalaben syrup wanda yasha da wanda bema bud'asuba yai duk yasa a shara.
Tareda gark'ame K'ofar d'akin nasa danma karwani yaxo yadameshi.

*Washegari*
Da asuba na idar da Sallah, Liman yayi khud' ar daya saba, wadda duk tak'ara Sanyayama Mukhtar da jiki. Seda gari yafara shaaa, kowa yai Hanyar gidansa.
Mustapha da Abbannasu sunrigashi shiga gida, k'arar rufe k'ofar get inne yajuyo dasu. Azatansu Mlm,Madu megadine, ganin Mukhtar cikin fara k'al in Jalabiyya, ba k'aramin mamaki sukajiba.
Musamman Abban nasu, tsayawa yai kawai yana binsa da ido. Bek'ara Mamakiba seda yaji Mukhtar in yadurk'usa yana Abba barka da asuba, be amsaba yaigaba abinsa. Ganin haka yasa Mukhtar in mikeya, suka Musabaha da Musthapa. Shima yanata mamakin yaushe rabon da sugan yatashi da asuba ma balle haryaje masallaci. Kowa yai hanyar d'akinsa. Dukda Mukhtar yaso gayamada abinda yasameshi.

Abbansu kuwa murna fal ciki yashiga gida yana bama hajia Uwani labarin d'annasu, tareda Adduan Allah yasa Adduar da sukeyi ce ta amsu. Musamman Mukhtar d'in.

``` Wannan kenan```

Tsaye take abakin get in sch insu ```School of science```tana jiran Napep ko Taxi, dan yau lecture d'aya garesu.
Jidda Ja'o k'awarta tayafito ta tace tazo su sauketa. Murmushi Naja'atu tai tace suje kawai bakomai.
Karta 6ata musu lokaci ga napep nan zata hau yakaita. Tai musu godiya suka wuce.

Usman yana gefanta duk wani motsi dazatai idansa nakanta, tasha kamashi yana kallanta. Se yai fuska. Ita tarasa meta tare masa duk yabi ya takurata a 'yan kwanakinnan. Sam kuma da bata ganinshi. Seyanzun.
Fitsarin da take ta rik'ewa taji kamar yazubo. Ga napep yataho tanata tsaidashi, segani tai yatsaya agurinsa. Batasan sanda ta galla musu hararaba, tareda cuno d'an tsukakken bakinta.

Murmushi kawai yayi harseda kumatunsa ya lotsa, dan duk abinda take idanunsa nakanta. sukai magana dame napep in, yayo inda take, shigewa ciki kawai tai batare da ta fad'a masa ina zaikaitaba, seda sukai nisa tasanarmai da d'orayi Babba zai kaita.

*waye usman dinnanne*???

*Aneesa_didi*🍼🍉😜
Anisadidi.pun.bz
[2/18, 10:41 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*♡
*Na*
*Haleema G khaleel*

15-16

*Waye USMAN*??
*Usman d'ane ga Alh Muhammad Bello Galadima. Dabinai.
Asalinsu fulanin k'auyen Dabinai ne dake Gabasawa cikin jihar kano. Alh Muhammad bello da akafi kira da Bello Galadima. Shine Galadima nabakwai agarinnasu. Bayan rasuwar Mahaifinsa Malam Ishak Galadima, tinda yafara jinya se akabawa Bello Rikon,k'warya, saboda shine Namiji duk yayunsa Manya Matane. Seshi dasauran k'annansa.

Bayan Rasuwar Mahaifinsu, sarautar Galadiman tadawo kansa. Dukda shi besoba. Alokacin yana aiki a Ministry of Health.
Suna zaunane a Unguwar Sharad'a, Matan Aurensa Biyu.
Hajiya-Hafsatu itace Uwargidansa, 'ya'yanta shida.Yusra itace babba se Usman da k'annansa,
```

Abdullah, Sadiq, Anas da Shukra.

Itakuwa Amaryar tasa daka gwale ya aureta seyamaida ta Dabina. Da 'ya'yanta uku. Al,Ameen, Umaima da Hajara. Saboda su duk k'arshen mako yakeyi acan. Yatafi juma'a da yamma yadawo litinin dasafe.
Wataran kuma yatafi dasu hajiya Hafsatu da 'ya'yanta. In sun kwana biyu basujeba.

Mahaifinsu yadage akan karatun 'ya'yansa. Hatta Yusra babbar 'yarsa. Seda tafara nisa dakaratu sannan akamata Aure bisa yarjejeniya da akai da Abbas mijinta zebarta tak'arasa. Inda take karantar *Food science.* Ayanzu haka tana shirin shekarata 3.

Bayan Usman yai diploma a ```sch of science``` se mahaifinsu yaturashi Igbedion universty dake edo *Medcine nd Surgery* yai specializing a 6angaren Gynecoligist.
Usman dogon namijine, ba alamar kiba atattaare dashi. Wankan tarwad'ane hancinsa zarkaded'e kamar biro👃🏾 irin na fulanin Dabinai. cikin zagayayyiyar fuskarsa daukeda dara-daran,sexy idanuwansa. Da d'an faffad'an bakinsa.
B'oyayyen jiki ne dashi. Inkin ganshi bazakice yabama shekara 30 bayaba.

Dalilin Had'uwarsu da Naja'atu kuwa! " Visiting lecture yake zuwa" makarantar. Dan tunda yabarta ya k'udurce aransa seya taimakawa makaranta musamman 6angaren practical.
Idan yashige cikin d'aliban yana k'ara guide insu seka zata shima d'alibine. Baruwansa kowa nasane.

Wataran yashigo sch in dawuri.yasamu gurin zaman d'alibai yaxauna, kafin agama gyara office inda suke zama.
Ganinta yai tanata sauri kamar takifa. Kanta a k'asa, yai mamakin saurin metake haka? Abinda bakowana Malami ne yagama zuwaba. Inma tsoro take kartai missing lecture.
Wasu maza yagani su biyu abayanta."seda takusa shan kwana ta tsaya ta juyo.dukda rawar da jikinta yake. D'aya yakai hannu zai shafo fuskarta. Batasan sanda ta d'aga hannu tabashi mari a fuskaba.🙄. Niba 'yar iska bace irin yadda kukema sauran mata. So mind ur self tai wucewarta tabassu a tsaye. Cikeda takaici.

Usman Jiyai tai matuk'ar birgeshi, koba komai takare MARTABARTA. Ta 'ya mace ga nutsuwa a tattare da ita.
Tundaga lokacin yafara bibiyarta a sch har yagano awani depertment take. Seda yasan yayai yake zuwa depertment in kuma class insu. Yashige cikinsu kamar d'alibi.

Presentation zasiyi akan wani practical dasukai. Kowa anbashi mezeyi akai. Toseka cike wani foam daduk wani details inka har contact, anan yaga sunanta. *Naja'atu Abdul-mu'iz Auwal*.
Kawai sede taji yafad'o sunanta. Taita tunanin aina yasanta.
Hartakai ga *Yayi gamo* Abinda baitab'a tunanin zai sakeba.

*cigaban labari*

Naja'atu kuwa tana sauka daka napep naira d'ari tabashi tashige gida da sauri, ko chanjin bata tsaya kar6a ba.
Allah yataimaketa bakowa a toilet, tashige tanata sauke numfashi.
Seda tada nutsuwarta sannan takula da mutane a falon Innar.
Harara Innar ta biyota dashi. Suka gaisa da mutanen, tai cikin d'aki. Wanda ya bige Kamal ne sukazo dubashi tareda 'yan gidansu.

Mustapha daya tuk'osu , dan Mamantasu tace bazata hau tuk'in Mukhtar ba, seya k'ara hankali.(kujifa kamar MM Ateeqs ace baida hankali! Waya jawo😌 in bashiba).se shi yakasu su hud'u da iman.
Mustapha yabi Naja'atu da Kallo. Kamar betab'a ganin mace ba. Naja'atunce akwai shiga rai😂.

Koshima *Yayi gamo* irin na Usman galadima😍???

*Aneesa_didi*🍼🍉😳
Anisadidi.pun.bz
[2/18, 10:41 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKI RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

17-18

Hajiya Uwani tak'ara bawa Inna hak'uri. Tare da fad'in gangancine irin na yara. Siyita gaggawa acikin lamuransu.
Inna tace " Ai bakomai" haka Allah ya k'addaro saita faru. Bawanda ya isa yak'etare hukuncin ubangiji.

Sukai tahira kamar sun dad'e dasanin juna.
Mukhtar kuwa yabiyewa Kamal da Deedat, kaman wasu abokanansa. Deedat kuwa se farinciki yake za a d'anashi a mota.

Seda yasan yadda suka saki jiki dashi. Dawayo da dabara yatambayesu sunan, yayarsu. k'aramarfa? Yaya Samiha? Kamal yace yana karkatar dakai.
Samiha! Yamaimaita sunan. Dan baita6a jin irin sunanba.
Itace 'yar yarinyar dabatafi 16-17yrs ba. Amma har ta furta masa maganganunnan. Ya shafo gemunsa, yana tunanota lokacin datake tsiwa akan ya bige k'aninta.

Ya Mustapha kuwa yanata baza idanu yaga ta ina zata 6ullo. Yarinyar da ko sunanta beji an ambataba.
Ahaka har sukai masu sallama suka tafi. Bayan sun cikasu da abin arziki. Da nufin se Mukhtar in yadawo maida Kamal Asibiti.
A k'ofar da zata sadaka da waje, suka had'u da Ibrahim, sukai musabaha. Mukhtar yace Isma'il,

munzo duba jikin Kamal ne, Ibrahim yai murmushi, yace Ibrahim ne, Isma'il bedawoba. Da mamaki Mukhtar yace amma kunyi tsananin kama.

Ibrahim yace "Ai twins ne mu". No wonder kaman yai yawa. Sukai sallama yawuce yana mamakin dama akwai 'yan biyu maza masu kama haka!.

K'arfe 2na dare, ta idr da sallolinta, tanata addu'a. Harta idar. Jingina tai da jikin gadansu. Tajanyo hand-out inta ta Medical Rehabilitation, tana k'ara bibiyarta domin test in course in zasiyi a wayewar garin.

Vivration na hud'u kenan da wayarta tayi. Zatanta Alarm in data sakane, sa6anin tunaninta tagani.

Bak'uwar numba ce dabatasan wayeba. Kira aka kumayi, dukda haka batai received ba. Koma waye yagaji yabari. Da talatainin darennan adamu mutum da waya.

Kaman zata kashe wayan seta ajeta, tacigaba da karatunta.

Zim-zim taji wayar tayi alamun shigowar sak'o. Barinta tai batareda ta dubaba.

Ba ita ta runtsaba, seda tai sallar asbah ko Azkar bata iya k'arasawaba bacci yai awangaba da ita.

Inna inaji yau Ya,Naja bazata Makarantaba. Samiha tafad'a tana gyarawa Salim safar k'afarsa. Bayan sun karya sukaima Inna sallama sukatafi sch insu. Kuntau science acadamy.

Inna taga har takammala gyaran d'akin taiwa Kamal da Deedat wanka, har 8:30 ba Naja ba alamunta.

Dakinnasu tashiga, can tahangota a kan sallaya ta k'udun-dune tanata bacci abinta. Cikin ranta tace "ko lafiya"?. Bubbuga k'afarta tai tana Yayar-Salim2 lafiya kiketa bacci kobakida makarantar yau?. Ahanzarce Naja tatashi tana fad'in Hasbunallah Inna! Jiya karatu nazauna. Bayan nai Sallah bacci ya kwasheni. Tai zumbur ta mik'e. Tayani addu'a Inna test zami kuma 9 zamu shiga. Bashiri tai band'aki tai wanka ko futa bataiba. Agurguje tashirya cikin yellow Jallabiya, tayane kanta da purple mayafi.

Ruwan shayi kad'ai ta kurb'a tai waje.tanata addua. Yau Ko tsayawa bataiba, tana tafiya tasamu Napep tashiga sai school.

Dashigarta makarantar, Jidda Ja'o tanema a waya tasanar mata da venue in daza ai test in tunda general course ne basu kad'ai zasiba harda 'yan wasu department in.

Kai tsaye tai A,block. Gabanta yai mugun bugawa ganin mutane atsaitsaye, gashi duk bataga 'yan class insuba. seda taje kusada wasu taji ashe venue inne yacika. Aka fara rarrabasu, har akazo inda take.

Kwankwasiyya,block akace suje. Duk nawarta setaji yau tanata sauri. Gashi duk bata saba da wanda suke tareba. Suka fara shigewa. Seda tafuto da abubuwan dazatai test in dasu sannan tashiga. Ta ajiye sch bag inta tanemi seat tazauna.

Seda duk suka nutsu sannan tafahimci waye  invigilator innasu.
Todama wannan ba student bane? Tafad'i tana kalloshi. Caraf idanunsu yahad'u dana juna! Saurin sunkwi dakai tayi, tahau rubuta sunanta. Ganin irin kallan dayake mata.

Mss xoxo ko kingane waye???😜

*Aneesa_didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:45 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*....♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

1️⃣9️⃣-2️⃣0️⃣

Har tayi ta kammala bata k'ara kallo inda yakeba.
Daya sungaggama, ganin anfara submit yasa itama ta mik'a tai waje batareda takalleshiba.

Common room tanufa, taga kosu Jidda sunacan, dabata gansuba tazauna zaman jiransu, "dan se 12 sukeda lecture.

Wayanta ta 'dauko tana duba lokaci, alamu tagani na message da bata bu'daba. Ganitai tin karfe uku saura nadare aka turo sak'on,

"Kiyi karatu sosai, kuma banda ru'dewa, Allah yabada sa'a"

Abinda tagani cikin,sak'on kenan batareda tagane mai number ba.
Tana zaune harsu Jidda da Meeno suka k'araso, sunata comment akan test in da akai yanzun. Itakuwa se murmusawa take, meeno tace aidole ki dara, "tinda bame takura ne yai maku invigilating ba". Tafa'da cikin sigar wasa.

K'arar shigowar sak'o ne, yadakatar da ita daka dariyar da take.

"Hope bakiji wuyan test inba? Dukda naga kinyi saurin gamawa".

Number sak'on jiyace. Itakuma batasan wayeba. Komadai waye yagaji yabari. Tinda ba amsa.
Yatsine fuska tai ta aje wayan, tareda kishingi'da, tanajin su Jidda sunata surutu taimusu shiru kamar me bacci. Har bacci mai dad'i yakwasheta.

Seda 12 tayi suka tasheta dansu tafi class za a shiga lecture, yunwa taji tana saka'dar ta, harsun shiga class ganin Malamin nasu baik'arasoba wato Malam Es-Bala tace Jidda tarakata koda biscuit ne tasiyo, zaro ido Jidda tai tace " Sokike mi biyu babu? Kinsan Es,Bala baya

missing yin lecture" sede yazoko a makare,
Yunwa nakeji Jidda ruwan tea kad'ai nakur6a nafito. "Kinga in yashigo bezama lallai nafahimci karatun ba". Gashi ba futa zai dawuriba. Bari inyi sauru nadawo ga seat ina nan, inkuma kannadawo yashigo to shikenan.

Biscuit da ruwa tasiyo. Aikuwa tana doso class in taji muryarsa, tabbacin yashigo. Juyawa kawai tai tatafi masallaci. Taci biscuit inta tasha ruwa, (kun sandai rayuwar makaranta zuma da mad'aci ce😂 sai hakuri). Ita dama bamaisan yawan cin abincin cafteria ceba. Ko zuwa sukai saidai taci wainar fulawa😋 itama ba kullumba.

Sallah tai tanata zaman jiransu, basu suka fito ba sai 1:40 narana. Taji takaici sosai narashin samun lecture dabatai ba.
Sukai sallah suka hau cin abinci suma. Fita tai tabarsu. Tatafi gurin Aminu wani 'dan ajinsu, dan yakoya mata abinda akai batanan. Kamin 2:30 su shiga lecture insu ta k'arshe a ranar.

Dr Usman kuwa, k'udur cewa yai aransa yau seya bita yagano a inda take. Wurin Iyayenta direct zashi, ji yake yayi mata akaro na biyu🙀 (tofah! Wace ta farkon🤔). Kiran gaggawa ne yasameshi, daka ministry yazo jikin mahaifinsa yatashi, hankali tashe yatafi batareda yayi abinda ya k'udurtaba.

Se 5 na yamma tada gida, kantai komi seda tacika cikinta. Tai wanka.
Tana zaune a barandar k'ofar part insu. Itada Deedat da Kamal ansamai shinfid'a awaje kafin magriba. su Samiha da Salim suna Islamiyya, gani sukai anata shigo da Akwatuna, harsaida aka shigo da guda 7.

Inna Ya,haris ya kirata, bayan ya zura kansa a k'ofar d'akin, "ki fito ga kayan lefan Labiba, anfara kawo nata.
"Masha Allah" inna ta ambata. Yace maza nema suka kawo. Tafurta ai hakan yayi daidai. Allah yasa alkairy yasa ayi damu. Saura naka inji Inna. Yace ai duk tare za a had'a mu shudan, Labiba Musa Ni Dauda Nasir da Mabruka  duk za ai. Kowa yasamu sauk'i. Yanzunma jiran 'yan gidansu Saurayin Mabruka. Dankomi ayi atare. Gaskia yayi kyau hakan. Suka ga kayan Labiban tareda sanya Albarka.

Alhamis da yamma basuda islamiyya, Naja'atu tana 'daki tana guga. Deedat Inna sun fita dashi.
Samiha ce zaune itada Kamal dayafara takawa yanzu kad'an kad'an, suna kallo.

Sallama sukaji ta amsa seganin wanda ya bige Kamal da mota tayi, shida Salim sunshigo tareda kannansa Iman da Ummi. Amsa Sallamar tayi tareda yi masu iso. Tinda tagansu da Salim tasan seda suka gaisa da babansu yabasu damar shigowa.
Gaisawa sukai bayan taka masu ruwa. Mukhtar se satan kallanta yake. Shidai yarinyar tana birgeshi, da alamun bazata amshi rainiba. Yanata sak'ar zuci gameda ita. Samiha kuwa

sunata hirar karatu itada ummi, harsuka gane mates nesu. Kiran Naja'atu tai suka gaisa itama, tasanar masu ai Innar batanan. Sungode kuma Kamal yaji sauki sosai. Sede addu'ar Allah yakiyaye gaba.

Har sukai sallama zasu tafi, dukda Mukhtar yaso sun'dan zauna, dan yau tasake sunata hira, ya fahimci ashe *kallan kitse* yakema rogo saukin kai gareta. Amma zaik'ara gwadawa.

Aneesa_didi🍼🍉😜
[2/18, 10:47 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*.....♡
*Na*
*Haleema g Khaleel*

2️⃣1️⃣-2️⃣2️⃣

Shirye-Shiryen Biki ake tayi dako kowane 6angare, musamman gidan Alh Abdul-mu'iz Auwal, dasuka da'de basi biki ba. Gashi kuma bikin mutum shida.
Sauran 'yan matan gidan ma dabandasu a Auren suma ba abarsu abayaba. Kaman su Samiha da Juwairyya sa 'arta se Madina da Bahijja. Itakuwa Naja'atu batada sako mace se namiji. Hakan yasa seta shiga cikin su Juwairiyya, dukda inka gansu zakai tunanin sun girmeta. Dan sunfita jiki.

Abubuwa suka had'e mata dan sunkusa fara exam in 1st semester. Test-Test kawai suke zubawa. Tana dawowa daka Makaranta ko wanka bataiba su Juwairyya k'annanta suka sata a gaba sesun tafi k'unshi da saloon dak'yar suka bari taci abinci suka tafi.

Saloon suka fara zuwa akai musu wash and set. Itakuma steaming akai mata. Dakanan suka tafi Salanta. Gidan k'unshi. Akai masu Lalle maikyau itadai Naja tafisan ja shi ka'dai akai mata. Se bayan Maghriba suka dawo gida. Gidan cike da mutane jikokin gidan da bak'i nanesa da suka fara zuwa. Dan gobe Alhamis zasu fara event in bikin da kamu . Gaggaisawa sukai tayi da 'yan uwa sannan tai 'daki dan tai wanka.
Tinaninta 'daya gobe k'arfe 2:30 Bio214 practical zai masu test, sunyi sunyi ayi dasafe yace shima bayanan dasafe. Haka suka hak'ura. Yanzu ita yazatai? Gashi indai bataje gurin kamunba abin zaizama magana.
Hakadai tana dan duba manual inta tana ha'da musu kayan sawarsu tinkan gidan yak'ara kacamewa da jama'a

Karfe 2 tashirya tatafi makarantar. Seda tagama rok'on inna in su Samiha sundawo tasasu sujirata sutafi tare. Dawuri zatai tafito.

Tsabar zumu'di ma, bakin lab in tatafi tazauna, har sauran 'yan class suka fara zuwa seda yaga

suntaru sannan ya bu'de musu lab in suka shiga.
Bata ta6a tunanin test in zatai sauk'i haka ba, kafin 3:30 tagama tabayar. Seda ta bari tai Sallar la'asar. Sannan sukai sallama dasu Jidda tamusu sallama kowa yai hanyarsa.

A inda tasaba tsayawa, anan tatsaya. Ganitai anyi parking da mota agabanta. Bata dai fahimci kowayeba. Juyar da kai tayi tana tarar Napep.
"Amincin Allah agareki our future Sonologist"
Taji ya fa'di haka.
Yau kuma tanan ka 6ullo? "Ta fa'di cikin ranta" dantagane muryan. Juyowa tai cike da tsiwa.
"Wai kai dan Allah maina tarema? Mikakeso dani? Duk komi nake idanka akai😙".
Tsayawa yai kawai yana binta da ido. Jiyake kamar yaha'data da kirjinshi. Koya rage abinda yakeji game da ita. " 4 the second time, Am deeply Madly in luv with you Naja'atu" gyara tsaiwa yai kamar badaka bakinshi kalaman suka fito ba.
Napep ta tsayar tashige dan ita abin nashima yafara bata tsoro.

Kaman mara zuciya kuwa shima yabi bayansu. Yaga inatake danshi tasama zai biyo mata. Ba irin samarin nanneba dazasu tsaya suna 6atama yarinya lokaci, daka baya kuma yazo bai auretaba.
Yayi aniyar komi bisa tafarkin sunnah zaibishi hatta zuwa zance sai yafara gabatar da kansa gurin iyayanta. Sannan zaikai kanta gareshi.

Lafiyar Allah suka kai gida. Tasauka tabashi kudin, shiga gida tai tindaka waje tafara ganin yara sunsha ankon bikin harma da manya anata tafiya gurin danba a gida zasiba.

Yana daka cikin motar yahangota har tashige gida. Kashe motar yai tareda gyara zama harse sunfito yaga kwalliyarta sannan yawuce.
Tab inshi ya'dauka yafara buga ```Candy crush```. Yanajin da'din game in. Cikeda nisha'di.

'Yar boko se yanzun? Ai seki sauri ki shirya anfara tafiya dan in aka tafi saidai kihau Napep. Yaya,Habiba ke fa'din haka, daka shigowarta. Gaisuwanma bata ida amsawaba tahau sababi😏. Sum-sum tawuce taname Allah ya kyauta.

Ankon material sukai iya matan gidan, kowacce tasha make-up.ni *Didi_Anees Kara zira kai kawai nake nagano Naja'atu.

Canna hangota cikin material innasu milk,colour daratsin golden, dinkin Bubu tadau light make up (kunsandai natural make-up yafi chau👄) tayana mayafinta golden akan kafa'da, se kamshi suke. Tana gyarawa Deedat takalminsa suka tafi. Yaya hafiz ne zai kaisu itada juwairyya dasu bahijja.
Futowa tai taga duk motocin compound in acike suke, waje tafito can taganosu gefan get insu, taja hannun Deedat suwuce, tirjewa yai yana nuna mata abu "shi tasiyamai" juyawa tai taga ashe mai san yoghurt ne, kiransa tai yazo yabashi.

Kamar an tsikareshi ya 'dago, ganinta yai tayi kyau ashe haka take! " *Fatabarakallahu Ahsanul qalik'een.*"da yaro yagansu da alama abu tasaimai. Suka wuce. Addu'a ya hau yi "Allah ya mallakamai wannan halita".
Nidai nace ameen👏🏼.

Awurin biki Amare sunsha kyau shiga iri daya sukai, bayan bu'da taro da addu'a aka hau shagalin biki. K'anne da yayunsu su sukai rabon abinci da seveniour.
Har aka kammala taro lafiya kowa yakoma gida. Kosu Naja ba abarsu sunda gidaba seda aka maida kowa sannan suma suka tafi.

Washe gari juma'a bayan sallar juma'a dubban jama'a suka shaida 'daurin Auren 'ya'ya 6 na Alh Abdul-mu'iz, a masallacin Jumu'a na Shaik J. Dayake Alh mutum ne na mutane. Sunga mutane kuwa.

Yau ba abinda zasi se dinner da angon Labiba Farouk suka shirya, a Xahra event, dayake 'dan unguwarsu ne a bayan gidansu yake. Mahaifinsa abokanaine da babansu. Har kuma zumincin yak'ara karfafuwa Silar auren 'Ya'yannasu.

Bayan sallar Isha kuwa motoci suka cika layin, dagani kasan bikin manyane.
'Yan mata mata kawai aka gayyata se yayunsu wasu daka ciki.
Su Samiha 'yan mata se shiiri suke, ya Najah yanxun kekuwa bazakiba? Juwairiyya tace.
Hmm barni kawai Juwai. Nagaji kuma kinsan exam ce a gabana.
Amma bari nashirya muje shikinan?
Yauwa yayarmu suka tafa.
Zaman jiranta sukai dukkowa suntafi. Sukai kwalliyarsu mai 'kayatarwa.

Se gurun 8:30 suka isa. Ganisukai maza dayawa, hakan yasa duk sukai rufaffan yafe.
Dukda haka saida wani yakulasu. Juwairiyya yake tabi. Sukai gaba suka barsu.
Samiha kamar ankirata ta 'dago caraf idanta yashiga nashi.

Mukhtar kuwa yasakarmata k'ayataccen murmushi, tasowa yai yanufosu, dukda a 'dan tsorace Samiha take. Yitai kamar bataganshiba.
Salamu alaikum yayanmu barka da dare, yataro? Naja'atu tai mamaki miyakashi nan.
"Abokin angone ni" yace shiyasa kuka ganni a anan. Anata shan shagali ko k'anwata?
Hmm kawai tace suka gaisa yatafi.

Haka aka gama shagalin bikin aka kai amare gidajensu. Sukuma angwayen duk kusada gida zasu zauna. Sedai muce Allah yabada zaman lafiya.

*Bayan sati biyu*

Da taimakon Allah da jajircewa ta kammala exams inta. Suka sami hutu. Hakan yabata damar tafiya Gusau dan zaga dangin Innarsu.

Usman yanzu gaba 'daya kak'i aure sabida wani dalili naka na daban! Mahaifinsa Alh M Bello yafa'da yana daka kwance.

Abba ba haka neba. "Sonake natsaya da k'afata" ba irin yadda akai a bayaba. In sha Allah Abba "dana samu aiki" dukda mu aikin ba wuya yakeba. Da akwai abinda nake jira.

Kaidai ba yaro bane daza ana lalla6inka akan kai Aure. Wani abunba saida Auren ake samunsa. Kiyi hakuri Mama. Adduar dai za a cigaba da tayamu. "Wata 'dalibata ce" amma nafiso afara tura manya tukun su tambayo. Kamin nan mun sasanta..

"Au dama batama san kanayiba? Maman tace.

Ba haka bane mama. Tasan ina santa. Kawaidai nafiso manya su shiga lamarin. To Madallah! Allah yashige gaba.

Baban yace inna k'ara warwarewa zamuje Dabinai. Se asan abinyi akan lamarin.

Afuwa pls makaranta. May be
Zaku 'danji shiru. Inkomi yai settln zancigaba.
Just need your Du'a

Didi luvs you all😘

Aneesa_didi🍼🍉😜
[2/18, 10:47 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*.....♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

2️⃣3️⃣-2️⃣4️⃣

*A Gusau*

A Unguwar Birnin-Ruwa ta yada zango, Gidan kakanninta ta sauka wato gidansu Innarsu. Abinka da jika tasamu tarba da karamci irin na Zamfarawa. Gashi dama ta da'de bata zoba.

Hajiya Ummi mahaifiyar Innarsu, mace mai kamala da sanin yakamata. Ga rik'o da addini. Babban 'danta ya gyara mata sashinta kamar na Amarya. Kawu Haruna kenan, ace warsa lokacine gara si mata wataran sai labari.

Aka cikata da kayan motsa baki. Su Hoce,  Tuwan'Bula, Amala da miyan ku'bewa,cima irin ta Zamfarawa de, taci wanda zata iya. Tamike a kujera, tinda fashin Sallah take. Se can yamma ta

tashi tai wanka. Tahau taya Ummin aikace aikace. Dukda tanada kishiya, da mijinsu ya rasu aka rabamusu gado kowa aka ware mata 6angarenta. Batare da wani ya takurawa waniba acikinsu.

Tun zuwan Naja'atu kawu Sa'ud yasamu hutu domin duk wani aikace-aikacen gidan shiyakeyi. Tinda yanzu shika'dai ne daya rage bai Aure ba. Komai baya bari Ummin tasu tayi, girki shara wanke-wanke duk ya iya shike mata, iyakaci tai wanka tai zamanta, wataran ma har mai yake shafamata. Kominsa a 'dakin yake, gado ma biyu na ummin da nasa a gefe. Makaranta ce kawai ke rabasu ko wata sabgar.

Tin Ummin tana fa'da har tagaji tabarshi, tasan dayai aure dole yabar mata 'dakin.
Zuwan Naja'atu nema yasashi yakoma kwana a falon ummin, da yai wanka zai shirya ya fice.

Naja'atu ba k'aramin jin da'din zaman gidan kakar tasu taiba, seda tai kwana4 ba inda taje.
A ranar datai kwana na biyarnema tafara zaga sauran dangi.
Gidan Gwaggo Balaraba, Kishiyar Kakartasu tafara zuwa ta yini. Sukai tahira abinsu. Itama tabata tsarabarta takoma wajen Ummi.

Washegari, ne taje gidan Kawu Haruna, da Kawu Bashir k'aninsa shi 'dab gwaggo Balarabane. dayake gida 'daya suke zaune., da nufin takwana biyu ko uku.
Da zuwanta kuwa suka gaggaisa da mutan gidan Anty Khadija matar Kawu bashir ta kar6eta hannu bibbiyu. "Tace tashiga 'dakin faccalatta Anty Sumayya, " matar Kawu Bashir sugaisa.

Da shigarta 'dakin suka gaisa da Anty Sumayyan, suka 'dan ta6a hira, tatashi zata koma 'dakin Anty khadijan, matar Kawu Bashir in tace "ta tsaya su gaisa da sister inta"
Hinduwy tahau kiranta🗣️ seda tai wajen sau uku ta amsa da Yep.
Tin asannan Naja'atu tasha jinin jikinta, topah ita kuma wannan wace iri ce?🙄 Take zancen zucinta ita ka'dai.

Fitowa Hinduwy n tayi cikin riga da skirt na atampa matsatstsu, irin 'dinkin nan, sewani yatsina take😣. "Kizo kugaisa da Naja"
Bak'uwa kukai kenan? Ah " 'yar yar Babansu Sadeeq ce dake kano"
Oh! Sannu pha✋🏾 ya kike? Tafa'di kaman anmata dole tanata danna waya ha'de da cin chewngum.

Lafia Naja tace, taiwa Anty khadijan sallama, abakin k'ofar falon sukai kici6us da Sadeeq babban 'dan Kawu Haruna. Ja dabaya tai tabashi hanya yawuce,
Hannu ya mik'a danyfin yakamo hannunta sugaisa, tawaske itafa dama batasan ha'duwarsu. Danshi haka yake, tinda yaje karatu ghana yadawo yafara wannan 'dabi'ar. Sauda dama ma inta ganshi bata yadda suke6e tare, dominshi kama mace ko Hugging inta bakomai ne a gurinsaba.

Ah ah Ya,Sadeeq, kamar yadda kowa yake cemasa. " ashe kana gari,?"
Murmushi yasaki yace: "mutan Kano ne yau agidan namu?
Ai nakwan biyuma tamaidamasa.
Koda yake banje gidan Umminba kwana biyu damun ha'du.

"Ya Sch yasu Inna dakowa da kowa? Inasu 'yan biyun inna?"

Alhamdulillah! Kowa lafiya, sunanan suna gaidaku. "'Yan biyuma Abekuta zasu tafi karatu"
That good haka akeso ai mutara 'yan boko dayawa a Family.

Hmm tace "Allah de yasa Albarka"

Tsuuuuuuuu😚 sukaji anja tsaki! Tawuce fuuuuu kaman wata iska😂 Hinduwy ce ganin Ya,Sadeeq in data mato akansa yanzu yashigo ko inda take bai kallaba. Sabida ganin wannan Langen cousing intasa.(Naja'atu Lange😝) zatai maganinsu amma.

Naja'atu datagan haka tai saurin tak'aita hirattasu, takoma wurin Anty Sumayyan da suke kiranta da Momy.

Kwana biyun datai kowa se sanbarka yake da zuwanta. Domin komi yimasu take ba k'yashi ko bak'in ciki. Sa6anin Hinduwy dako kallan arziki bata samu daka gareta. Duk wata hanya dazatabi ta janye ya,Sadeeq tanayi, shigar matsunce, kayan dazasi bayyana tudu da kwarinta duk yi take koya biye mata da zarar yaga Naja zai rabu da ita.
Naja taita mamakin Hali irin na Hinduwy, ke gida bana ubankiba amma kinzo kin zak'e. Allah dai ya shirya

Tanayin kwana biyar tai shirin tafiya, sukai bankwana dukda sunso tak'arasa sati, ita kua taki yadda tunda hutun nata bawani yawane dashi ba. Suka cikata da kayan Arziki. Anty khadija kuwa kayan shafa da makeup tabata. Dakyar Hinduwy ta amsa sallamarta, (se kuma wani jik'on my Hindu😂😘)

*Dabinai kano*

Bayan Alh Bello galadima yasamu sauk'i, da k'warin jiki, dakansa yaje Dabinai yasamu kannansa, Baba Saminu da Baba Sani, wanda yake kulada gidan idan bayanan.
Yasanar musu gameda abinda ketafe dashi. Duk da shi Baba saminu yaso anhada Auren zuminci da Maryama 'yarsa da Usman 'din. Amma haka yaja bakinsa yaishiru. Sukai fatan Alkairy da nufin wani satin zasuje cikin garin, gidansu yarinyar da Usman in yakeso. Domin ai zancen manya.
Se muce Allah yanuna mana.
**********

Kawu Sa'ud ne ya'dakkota daka gidan Kawu Harunan. Dukda taso yakaita unguwar  Gada-Biyu, gidan 'yar Autar su Innar tasu mace, Anty Husna ganin yamma tayi yace: "tabari gobe taje setai mata kwana biyu" tinda sati biyu zatai.
Da shigarsu gidan ummi tana tsakar gida tana Alwala, tai masu sannu da zuwa, itama ta aje kayanta tashiga bayi kama ruwa. Shima kawu Sa'ud yai waje

Alwala tayi tashige 'dakin Ummin suka zauna kan atada sallar subi Jam'i.

Bayan sallar isha sungama cin abinci itada ummin, Tuwan shinkafa ne da Kawu Sa'ud in yayi kamin yaje 'daukota, yabarma Ummi Miyar Shuwaka da taji Nama zuk'u-zuk'u tak'arasa.
Kwashe kayan tayi tamaida kitchen. Tadawo tazauna suna kallo, Sallama sukaji ta amsa tareda rage volume in tv.
Kawu Sa'ud ne tareda Yunus abokinsa.
Suka k'arasa shigowa falon Ummin. Har k'asa ya duk'a yagaida Ummin. Malam Yunusa ne yau a gidannamu?
Ya amsa da fara'arshi. Belura da su biyu ke zauneba. Seda yaji Sassanyar muryar Naja'atu har cikin kansa tana gaidashi. Amsawa yai a kasalance tareda kai idanunsa kanta.
Wata kyakkyawar bak'ar yarinya idanunsa suka ganemai. Tamkar Sa'ud, sedai shi yafita Haske da tsayi. duk yadda akai *Jininsu 'daya*(My Anee_luv😘).

Amma ya akai baisantaba. Kuma bai ta6a ganin taba.??

Wanga Samrayi Kodai shima yayi Gamo ne😂😍??? Wayaga Rk&Madhubala😜

*Didi_Aneesa*🍼🍉😜
Anisadidi.pun.bz
[2/18, 10:47 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA....* ♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

2️⃣5️⃣-2️⃣6️⃣

Hararарsa tai tareda sunkwi dakai, ganin irin kallon dayake mata,

'Dakin Ummi tai nufin shiga, Kawu Sa'ud yace taka musu Abinci. Bayadda ta iya haka ta'dauko flask guda biyu ha'de da plate da chokula. Taka ta ajiye seda yasata zuba musu. Sannan tashige ciki, dan duk tatakure da kallan da Yunus in yake binta dashi.

A wayewar garin, tashirya tsaf. Tazauna zaman jiran Kawu Sa'ud in zai kaita Gada-Biyu gidan Anty Husna, yaje 'dauko motan gidan dasuke ajewa.

Tsiya Ummin take tamata dantace mata ita batada Saurayi. "An daiyi Budurwar banza" kamarke ace bakida Saurayi kode korarsu kike? "Hmm habade Ummi kawai baruwana dasu".

Gashi nikuma banda miji bare najona masa ke. "Allah ma yakiyaye na auri tsoho".

Aikuwade maga irin mijin naki. "Zakuwa kiganshi zanka'de'de"

Allah de ya nuna mana wannan rana dazanga Auranki 'yar jikalle.

"Assalamu Alaikum"

Sallamar Yunus ta katsesu,

Wa alaikumus salam.

Ummi tace "shigo mana Malam Yunus".

Ummi barka da safiya ya gida? Alhamdulillah. Ya mutan gidan?

Lafiya lau suna gaidaki.

"To madallah"

Sa'udun yaje 'dauko mota anan baya. Kajirashi. Gidan Husna ma zaikai Naja'atu.

Se asannan Najan tagaisheshi. Ya amsa cikeda fara'a.

Ummi nadawo Sa'ud yace. "Au 'dan halak yak'i ambato kajishima ya dawo"

A ah! Abokina yaushe kashigo? Yamik'a mai hannu suka chafke. Futama zanyi bara in'dan zuba ruwa. Daughter kina ina sry kinji bari nai wanka.

Kai kawu danAllah kabari inka dawo kayi. Aibawanda zai ganka, "toke haka zaki tafi baki wankaba" salon budurwata taganni ba wanka" kaga shikinanma sainaga antyn tawa, tafa'da tana murmushi. Aikam ba ayi hakaba Yunus yasako baki shima, "kidaiyi hakuri k'anwarmu yayi wankan seya kaiki ko? Nima nayi rakiya".

Shikinan karka da'de kawu. Suka fice yana fa'din "yanzu zaifito suje".

Tak'ara tattarewa Ummi gidan dukda bawani datti yaiba.

Basu sukaje gidan Husnanba saiwajen 12 na rana, Anty Husna tai matuk'ar farin cikin zuwanta, Naja ta tausaya mata ganin Tsohon cikin dake jikinta Haihuwa yau ko gobe, dasuka gaisa Kawu Sa'ud yaimata Sallama yatafi yana mamakin girman ciki irin na Husna.

Wasa takeda Khaleefa 'dan Anty Husnan, yaro 'dan shekara biyu da 'doriya, cikin kwana biyun datai sukai sabo sosai, abinka dame san yara da juriya da dabdalarsu.

Bayan tagama duk ayyukan gidan, ta 'dora musu girki. Shiru-shiru taji bata fito ba, seta bari cewa Bacci Antyn tata tasamu. Ganin har tagama girkin ranar, lokacin Sallah yayi bata fitoba, shiga 'dakin tayi da Sallama, ganin Antyn tata tayi durk'ushe, abakin gado. "Subhanallah" Anty lafia. Hmm kawai tace da ita. Ganin tarasa yaza tayi yasa tabugawa kawu Sa'ud waya yagayama Ummi Anty husna ba lafiya.

Cikin mintunan dabasu fi Arba'in na, saigasu shida Ummi, tanata mata addu'a, taha'da mata duk

kayayyakin Sa'ud yakaisu asibitin datake zuwa. Dan mijinta baya gari. Ita kanta Ummin batai tunanin watan haihuwar Autar tata yatsayaba.

Naja'atu kuwa sai kuka take rungume da Khaleefa, dama haka haihuwar take, lallai iyayenmu sunyi k'ok'ari. Taji tasake san Innarsu ha'de da jinjina mata.
(Luv u my Innarmu. Mom like no other😍😘).

Tasha wuya sosai, sannan tahaifi 'diyarta mace, akai tawaya anagayawa 'yan uwa da abokan arziki. Kansu dawo gidan har mahaifiyar mijinta da k'annansa sunzo gidan, seganinsu kawai sukayi.

saboda haihuwar Naja'atu tazauna se bayan suna.

*Kano*
Kamar yadda suka zartar, sati na zagayowa, Baba Sani da Baba Saminu, sukaje gidan Alh Abdul-mu'iz, Usman 'din dakansa yai musu rakiyar. Baban nasu kuwa yakar6esu da karamci irin na Kanawa, suka rattabo meke tafe dasu, "'Dansu yaga 'yarsa kuma yanaso". Domin subi k'a'idar musulunci yasa suka zo k'afa da k'afa, nemar masa izinin zaifara zuwa gurin ita yarinyar. Alh kuwa yai farinciki, tareda yarda da nagartar yaron, sawa yai akira Usman in yaganshi. Baba Sani yakirashi awaya, yazo yarisuna yagaida Alh Abdul-mu'iz cikeda girmamawa dajin nauyi. Yamasa 'yan tambayoyi, duk ya amsa, yasanar musu da Najan ma batanan taje ziyarar dangin Mahaifiyarta a Gusau.
Yamasu sallama yai waje. Basu tafiba saida suka bada ku'din zance. Tinda bawani lokaci sukeso a 'diba ba. Gaisuwa suka k'ara irinta manya, sannan suka rabu sunata zuba godia. Shi kuma Alh yashiga cikin gidan yasanar musu, kowa saida yai mamaki, bama Inna da bata ta'ba ji koda wasa Najan tai maganar Usman dinba. Amma wai gashi harda ka ku'din zance. Addua tashiga yi Allah yatabbatar da alkairi koma menene.
(Topha ita amaryar bama tasaniba maji magani dai).
*************

Ana i gobe suna duk taha'da komatsanta waje guda, ranar Suna kuwa, suna akai irin namasu rufin asiri ba alamun k'arya aciki, yarinya taci sunan Raheena.
Aranar sunan da daddare tatafi gidan Ummi dan gobe zatai sammakon tafia kano, anriga ankoma Sch shiyasa zata tafi. Kawu Sa'ud shi yamaidasu gida ita da Goggo, dan Ummi k'in zuwa sunan tayi. Jitai kamar kada surabu dasu Anty Husnan, barema Khaleefa boy inta hadda guntun hawayenta.

K'arfe 9 na safe, bayan sunyi karin kumallan safe, Ummi taita mata Nasiha akan rayuwa da kukanta sukai sallama da Ummin, tareda fatan Alkairy gaba 'dayansu. Suka ha'da mata tsaraba fal.
kawu Sa'ud yakaita tasha yabiya mata ku'din motar sai kano ta dabo timbin giwa.

*Aneesa_didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:47 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

27-28

Sassanyar iskar data chanja ce ta tabbatar da sun shigo Kano, a tashar mota ta Kano,line aka sauk'esu.

Drop in Taxi tayi har gida, yasauk'eta abakin Get insu, kayanta tafara shigarwa ciki, sannan ta mik'a masa ku'din yatafi.
Bakowa a harabar gidan, yaran duk suna makaranta, manyan kuma yawanci suna gurin sana'arsu. Da sallama tashiga cikin gidan, Deedat da wasu yara dabata gane suwaye ba sunata wasa, muryarta da Deedat yajice yasashi tahowa da gudunsa ya 'dafeta "oyoyo yaya Najata". Oyoyo autan Inna Deedat 'dina, suka sa dariya, ajeshi tai yai 'dakin Innar da gudu.

'Dakunan sauran matan gidan ta shishshiga, suka gaisa sannan tai 'dakin Inna. Tanata mamaki jin Gwaggwo Safiya, takirata da Amarya hadda Allah yasa akairy, yasa ayi dasu. To yaushe tazama Amaryar? Kowani abun yafaru batanan? Duk wa'dannan tambayoyin bata da me bata amsa sai Inna, jiki salu6e tashiga falon Inna, a kujera ta zube, tanata maida numfashi kamar wadda tai gudun shekara.
Inna ta futo daka 'daki tana "lafiyarki kuwa yayar Salim naganki haka?".
Seda ta rusuna tagaida Innar, tace lafiya lau kawai gajiyar hanyace. Sannu to yakika barosu? Ina masu jego? Ah tagayamin munje kasuwane lokacin da k'annan Abban Khaleefa, sunanan lafiya duka. Duk suna gaidaku har matansu Kawu Haruna da Kawu Bashir, Ummi ma tace gawani magani nan wai kitafasa mana dukanmu muna sha. Allah sarki Ummi, yajikin nata kuwa? "Alhamdulillah Inna dan taji sauk'i sosai" kawu Sa'ud wankane kawai baya mata. "Ina ruwan Sa'ud, nagadai yazasu rabu da Ummi, wannan shak'uwa tasu."
Ai Inna nagayamasa kawai inyatashi auren yai zamansa a gidan, yasa dariya yaga kamar wasa nake masa. Yacede zai duba. Allah dai yai mana jagora Innar tafa'da tafita zuwa 'dakin Babannasu.

Sallah kawai tayi tahau bacci, k'arar da Samiha tasane yasata farkawa agigice, ganin Samiha tai tanata tsalle ha'de da "ki'da da jikin wardrobb insu tana Wellcome back Amaryarmu, mata agidan Ya,Usman". Tanatayi. Binta kawai Naja take da ido, se yanxun tafara ```Tuna baya```{Anty sumy takori} tatuno duk irin yadda sukayi da Usman 'din, tanan ya 6ullo kenan. Jitai hawaye yana bin kumatunta dabata tantance namenene ba. Bak'in-ciki ne ko Farin-ciki??.

Ganin tafara hawaye yasa Samiha daidaita kanta, zamatai akusada ita tafara bata hak'uri, Naja

kuwa murya na rawa tahau tambayar Samiha meya faru dabatanan? Zayyano mata komai tayi, bata 6oyeba. Murmushi tai wanda dakajinsa na yak'e ne. Allah yashige gaba shikinan, tai ban'daki tabar Samihan hangame da baki.

Da maghriba, suna zaune a falon, Inna ta wawwarewa kowa tsarabarsa, aka kaimusu. Sungama cin abinci Inna takira Naja'atu, alokacin suka warwarewa juna duk abinda ake ciki. Naja bata musaba ta amsa. ```Tunda dama iyaye keda right dazasu za6awa 'yarsu budurwa mijin Aure.``` iyayen iyayansuma da akaimusu auren basusan mazajenba sun zauna maiya samesu, gashi kuma har akasami wa'danda suka kasu duniya. Balle ita tasan wayema dazata Aura.

Albarka Innar taita sakamata ha'de da fatan Alkairy a rayuwarsu duka. Sukaita hira abinsu, hakan ba k'aramin kwantarmata da hankali yaiba.

Bayan isha, dasuka ci Abinci suka gyara gurin, da taimakon Samiha suka gyara kayanta, taha'da duk abinda zata buk'ata, dan gobe dawuri zata shiga sch tanemi time table, sun shiga final semester se sun dage. Kowa yanemi makwancinsa ya kwanta.

Wannan kenan.

Usman bek'ara kiranta a wayaba tunda akace batanan, koda aka koma sch dayaga bata dawoba, ya kar6an mata time table, Lectures in datai missing yasamammata Hand-out da manual, wasu har jotting yayiyyimata ajiki. Duk yaha'da yasa a leda yabawa su meenoh da Jidda Ja'o subata watak'ila kozata shigo shi bayanan. Suma sunyi mamaki daganin haka. Seda yace musu ma shi Visitin lec ne suka k'ara mamakantuwa.

Da safe duk suka shirya suna Karin,kumallon safe suka fice, har Deedat ansashi awata Islamiyya tasafe. Inna ka'dai suka bari a 'dakin.

Su biyar duka suka tafi a Napep aka sauk'esu a Kuntau, itama aka sauketa aka wuce da Fawad Al-Azhar shi acan yake.

Kamar sun ha'da baki suka ha'du da Meenoh. Seda sukaje class suka ha'du da Jidda Ja'o sannan su Meeno suka gaggaya mata abubuwan da akai batanan. Suka mik'a mata sak'on da Usman yabadar subata. Amsa tai taimusu godiya dukda tasha mamakin zak'ewa irin tasa.

Lectures sukai tayi babu wani interval sosai, saboda semester ta chanja.

K'arfe biyar suka tashi, sunzo fita abakin get taganshi se asannanma tasan yana cikin Makarantar dan sam bata ganshiba se yanzu.

Matafiya kuma tafiya ba sallama? Shiru tai kamar bada ita yake ba. Har suka fita wajen makarantar. Ba abinda yadameshi. Yanata janta da hira.

Seda taga idanu zasi musu yawa tasakammai wani mischevious smile, jiyai kamar yarungumota ajikinsa, amma babu halin haka.

"Kayi hak'uri ka tafi"
Babu halin sauraranka anan.

Badan yasoba yajuya yatafi. Yana mai farin cikin yau Queen of Heart inshi tamasa magana.

*Didi_Aneesa*🍼🍉😜
Anisadidi.pun.bz
[2/18, 10:47 AM] +234 703 962 5239: 11/11, 3:47PM Didisco
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....* ♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

29-30

Dawowarta kenan tazo wucewa ta k'ofar part in Babansu, Alh yayo kiranta dayaga wucewarta, Sallama taimasa tarusuna tagaidashi cikin ladabi da girmamawa daya kamata duk wani 'da nagari yayiwa Iyayensa.
Suka gaisa ha'de da raha kamar ba 'diyarsaba. Dan yana tsananin san Naja'atu sabida biyayyarta agaresh da hak'urinta.

Naja'atu yakira sunanta. Kiyi hak'uri namiki laifi, "Subhanallah" Baba dan Allah kadena fa'din haka, kana da damar dazaka bani kowana umarnine nabi, in dai ba sa6awa mahalicci neba, matuk'ar inaso inga Haske a rayuwata.
Alhamdulillah! Alh yace "Abinda yasa kenan banji 'dar ba na amshi ku'dinsu nasan bazakiban kunya ba".

Amma dole innemi amincewarki inkin yadda Alhamdulillah. Inkuma bakyasanshi, se amaida musu da ku'dinsu. Yace "kin amince naja'atu koba kyaso?
Sunkuyar dakai tayi ta'dan saki gajeren murmushi, abinka da manya kuma dama *(```Amincewar Budurwa shine Shurunta, Bazawara kuma Maganarta```)*.

Alhamdulillah Alh yace, "Allah yayi miki albarka yasa alkairy arayuwarki yasa kigama lafiya". Ameen Baba. Yayiy yimata nasiha ha'de da yaba Nagartar yaron. Yauwa tashi kije, kituran Innar taki. To Baba nagode.

Sanyi taji zuciyarta tana mata, dukda dai ba sansa takeba, amma zatai ta addu'ar neman za6in Allah tai sallama tashiga 'dakin Innar.

Inna Baba yana kiranki, har kindawo, ah daka gurin baban nake to ina zuwa, tanufi 'dakin Alh.
Zamatai da nufin tahuta, kafin lokacin Sallah yayi, wayarta tashiga k'arar *Antudd kilani Rabbil janna...*, kaman bazata 'dagaba taji da'din kwanciyar datai, mik'a hannu tai tajanyo jakarta, wayan tazaro tai Reciev batare da ta duba wayeba.

Nannauyar ajiyar zuciya taji a kunnanta, "Amincin Allah yatabbata agareki Sanyin idaniya tauraruwa mai haske acikin taurari"

Tare dakai amma dukni ka'dai wanna kirarin, tasamu kanta da fa'da. "Aikinfi hakama words can express how spcl you are" murmushi tayi, tamasa godia, balaife ta 'dan saki jiki sukai hira, dukda rabi hirannasu akan karatune.

Seda zasi hang up yace dole tai fixing date da time dazaizo har gida, kunya ta lullu6eta kaman yana ganinta. Wai yau aganta da namiji tana zance a gida yazatai? "Kinyi shiru kobaki so nazo? A a kawai dai kaban time zan fiddama randa zakazo, "ok tom no prob amma fa kada ki waladdani".

Allah bazan wahalar kaba, but sekamin uzri kaga sch yanzu ta'dau zafi last semester innan. "Hakane kada kidamu, kita Addu'a dai akuma dage, Allah yabaku sa'a".

Ameen nagode Allah yai jagora yace Ameen sukai hang up wayan yanata farinciki. Hadda ```Sujudu shshukur/sujjadar godia```. Dan tsantsan farincikim daya samu kanshi aciki.

Seda yai sallah Isha sannan yashiga gidan, Yanata bu'da hak'ora, Ah A "ko tallan maclean kafarane?" Maman tasu tace tana k'aremai kallo, kokuma Aikinne yasamu?

Adai tayamu da Addua Mama komai yakusa kammaluwa in Allah yayarda, "Allah ya yarda yatabbatar da alkairy, ai haka akeso.

Jiyai yana jin nauyinta, be iya gayamata komaiba akan Naja'atun 'daukar Abincinsa yai kawai yanufi 'dakinsa.

Shirin Duniya tumbin giya takeji agidan Radio, tana zaune akan sallaya gefanta kayan karatuntane, Tirrrrr taji 'yar Nokia tata tayi, message ne ya shigo.

"Nasamu kaina dajin kunyar Mama, nakasa gayamata komi dangane dake, dukda a 'dokance take taji harma gani daka kyakykyawar Surukartata."

Tamaidamasa da
"Hmm topha inni cema ai bazan iya gayaba."

"Kema kenan dannasan bakece 'diya tafarkoba?"

"Marabarmu dasu sutafara haifa amma dani ake kunyan 'yar farin hmm.".

"Hakane amma kinsan ya za ai?

"Ah ah saika fa'da"

"Kawai zangayawa Matata wato uwargidanki ta fa'da mata."

"Mata kuma??

"Ah mana kobakisan inada Mata ba? Kishiryama gidan mai mata zaki"😉

Reply in dabata sake maidawaba, dama wannan yanada mata amma baigaya mata ba? Yanzu yazatai, gashi tarigada ta amsa a wurin Baba, da fasawa zatai, dan ita bata marmarin auren mai mata, kodan irin wuyar da Innarsu tasha, dukda bata yadda sanshi takeba.

Anya kuwa Naja'atu?
Kodai kinyi gamo? Kihine dai kawai😂!!!

Sory 4 late post
So many isues nakeda.
Afuwa plss makaranta ina k'aunarku duka. Allah bar zuminci.

*Aneesa_didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:48 AM] +234 703 962 5239: 13/11, 12:20PM Didi
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*31-32*

Ta dad'e tana mamaki, har sarkin iya sata yasaceta daka inda take.

Jin shirun yai yawa bata damai da reply ba, shikad'ai yaita dariya abinsa. "Nafara gano lagonki Queen of my Heart". Seda yai salloli da Addu'oinsa sannan yakwanta, da tunanin Naja'atu.
Abaya idan akace zaiso wata macen bayan Bilkisu bazai ta6a yadda ba, amma yanzu gashi daga had'uwarsu da ita komai ya chanja, yanzu yafahimci Soyayyar, duk zaman dasukai abubuwan dayakeji dangane da ita Tausayine, yanzune soyayya tai masa *Dabaibayi* taimasa kamun da saiya had'a da Addu'a, karta sashi a mawuyacin hali.

Jitai kaman ana magana akanta, tafarka da addu'a a bakinta, Innarsu tagani cikin yanayi, tayi k'ok'arin tashi amma takasa koda motsa k'afarta, Naja'atu tace "Inna miyasameki? Lafiyar Allah muka kwanta".
"Kamamin Naja kikaini band'aki" tayi mamakin jin Innar ta ambaci sunanta yau. Da taikamakon Allah tataimaka takaita band'aki, har alwala tai tadawo da ita kan sallaya tazaunar da ita, alwalan itama ta d'auro, taita nafilfili tana kai kukanta gun Rabbi da nemawa Innarsu

Afuwa.

Har aka kira assalatu, Innar daka zaune tai sallar, itama tai *Raka'atanul-Fajir*, ta d'ora da Sallar asuba.

Zamatai tanata zikiri, har gari yafara haske, data duba taga Inna tasamu bacci, tashitai tahau kintsa d'akin nasu, tasa Kamal, Salim sukai wanka taiwa Deedat, itama tayi, Samiha kuma duk tahad'a musu kayan karin safe, Inna tafarka tagaduk shinrya, suka gaidata tareda yajiki, addu'a tamusu sosai sannan suka tafi.

6angaren sauran mutan gidan suka biya, suka gaidasu tareda sanarmusu halin da Innar ke ciki, sabida halin rayuwa. Naja tace da Maman danAllah in Iya tazo tasa tataimakawa innan kafin sudawa. Suka tafi makaranta.

Wunin ranar haka tayi sukuku, dandai kawai makarantar suna zangon k'arshene, bataso tasake dawowa inta tafi kawai tatafi, wani sashen na zuciyarta tatuno yanda suka k'are da Usman adaren jiya. Jitai ma komi yafuta akanta, taita Allah Allah atasi.

Sunagama lectures in ranar ko Sallahr, la'asar bata tsaya tayiba tatafi gida, seda ta duba Innar hankalinta yad'an kwanta, sallah tai sannan tataimakawa Innar tai wanka tareda Alwala. Tashafeta damai tasamata kaya, abincima dak'yar taci kad'an.

Homework suke koya musu Fawad da Samiha, itakuma tana harhad'a musu kayan wanki da Unifoam insu,

Inna tana daga d'aki, tari yasark'eta, yitake ba k'ak'k'autawa, dagudu duk sukayo wurinta, me mik'o ruwa nayi masu sannu nayi, Naja dak'yar ta d'agota tanata hawaye, Fawad fita yai da sauri yaje ya fad'awa Babansu yanatareda Idrisa Dauda da Hafiz, atare duk suka shigo d'akin, shigowar Ibrahim kenan, yada daka wurin shirye-shiryen tafiya makarantarsu, Isma'il kuma bayanan.

Sukai ta mata sannu, abin kaman k'arashi ake, ganin haka yasa Alh yace akaita asibiti.

Asibitin Nasarawa aka kaita ```Emergency``` Dr,Badariyya itakeda duty a lokacin, aka kwantar da ita Drip tafara samata, tai mata 'yan tambayoyi, tarubuta magunguna da allura asiyo mata.

Ya,Hafiz da Ibrahim ne sukaje ```Pharmacy``` suka siyo magungunan da alluran aka bawa Inna maganin, allurar kuma akasa cikin drip in.

Abu kamar wasa jikin Inna yak'ara tsanani, dole aka bata gado. Naja ce ke kwana, dasafe kuma Isma'il da Ibrahim su wuni, tunda basu tafi Makarantar ba sukuma sauran k'annannasu sede akasu jefi-jefi saboda Makaranta.

Haka ta had'a da zuwa Makaranta da zaryar asibiti, tsawon sati biyu Ummin tama da Anty Husna saida Kawu Sa'ud yakawosu suka dubata..

*Bayan Wata d'aya*

Hankalinsu yakwanta ganin Innar tasamu lafiya, duk nacin da Usman keyi akan tayadda yazo taki, seda aka sallamosu sannan ta amince yazo harma yaduba Innar. Haka kuwa akayi, ranar batada Sch. Bayan la'asar yazo, suka gaisa da Alh, sannan tafito.

Akan bench suka zauna dasuka gaisane yake tambayarta miyasa take wahalar dashi haka? Hmmm tace "ni bana wahalar dakai miyasa kace haka?".
Hakane mana kowayanki nakira kullum akashe,
Kasande bana zama asalima bana cikin nutsuwa tinda kaga haka, se a 'yan kwanakinnan nasamu kaina. Amma kayi hkr,
Wane mutum ai "Amarya bata lefi kota mari uwargida".
Rufamin asiri "Bata marabane",.
Sukai tahira abinsu, tafahimci sauk'in hali gareshi, anan yagaya mata ainahin waneneshi, tsokanar ta yake amma yata6a Aure sede matar ta mutu yazo haihuwa ita da abinda kecikinta. Zam baki labarinta bayanzuba amma. Taimasa jaje, yashiga yaduba Innan, itama asannan taganshi.
Yamusu sallama yatafi. Itama tacigaba da harkokinta.

Mutara danjin cigaban labarin.

*Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:48 AM] +234 703 962 5239: [14/11, 3:41PM] Didi
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA......* ♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*33-34*

*Bayan wata biyar*
Takammala makarantar ```school of science``` cikin nasara, cikin lokacin sunyi shak'uwa sosai da Usman Galadima, duk rashin magana irin tata saida yai nasarar koyamata hira, musammanma dashi. Soyayya suke cike da aminci bege da k'aunar juna.

Dawowar yayansu, Bilal d'an Goggo Safiya daga karatu, a k'asar Ethopia inda ya had'a degree insa nabiyu, a 6angaren Agric, hakan yasa 'yan gidan suka shirya masa walima.
Tunda safe wasu daga cikin 'ya'yan gidan suka fara zuwa, anata harhad'a abubuwan dazasuyi.

Niyyarta a ranar taje gidansu Hafsa taga kayan lefanta. Amma walimar da aka shirya dole tahak'ura, badan tasoba. Har d'a da jika suka had'u gidan yacika mashaAllah, kowa ya hallara

sede wanda basa gari.

Yammacin ranar bayan gama Walimar,  Rumaisa yayarsu tasa Naja takai 'ya'yanta mata kitso su biyu, shiga d'aki tayi kamar taafashe da kuka. Ganin haka yasa Inna tambayarta "Allah Inna ni banasan shiga gidan Yawa.

Gashi yaya Rumaisa tace nakai Aisha da Nana, "kiyi hak'uri kikaisu.

"Haka tasasu agaba suka tafi, inta kaisu seta dawo in angama musu ta d'akkosu.

Gidan Yawa gidane dake cikin Unguwarsu, gidane dake d'auke da sassa daban-daban kowane 6angare da irin Sana'ar dasuke, wasu daga cikin mutan gidan kuma Bak'in ciki da hassada taimusu katutu.

Basa k'aunar subud'e idanu suga wani yafisu, inda wasu kuma suke Rayuwa dabasu da mai fad'a musu suji.

Sale d'ane agidan, yazo yace yanasan Bahijja, ita kuwa tai masa tatas gani shikansa baida wata cikakkiyar tarbiya, daya takura mata ma tahadashi da mazan gidansu sukai mai magana anyi d'auki badad'i bakad'anba, Dalilin dayasa suke cewa 'yan gidan su Naja'atu masu girmankai, dad'i da k'arin basa Auren talaka sai mai kud'i.

Yanzunma badan tasoba tashiga gidan kaisu kitson, tinda ayanzu channe kad'ai zata kaisu susami kitson.

Seda tai wuce-wucen hanya da lunguna duk acikin gidan, kanta kai 6angaren Magajiya mai kitso, dasallamarta tashiga sashen, ganin Magajiyar tai cikin shirin fita unguwa.

"Ah ah! Yau kune a gidan namu? Inji mai kitson

"Gaisawa sukai, Naja tace "bazasu samu kitson ba kenan naga fita zaki?

"Bakomai se ai musu ai tafad'i. "Masamu na karin safe.

"To angode inji Naja'atu ta mik'a mata kud'i da man kitson, tace zata dawo in angama ta d'aukesu.

"To shikenan sekin dawo.

Tin shigowarta suke ta munafincinta, sam bata kula dasuba, se yanzu dazata tafi, taga se hararartа wani Rabi'u yake, itadai tawucesu batace komaiba se Addu'a data karanto acikin ranta.

Gidansu Hafsa kawai tashiga, bata koma gidaba, suka bud'e dandalin hira ta shantake acan.

Yaya Rumaisa kuwa ganin magriba takusa basu dawoba, ta Aika Bahijja taganosu, dazuwanta angama musu kitson, suka taho.

"Innalillahi Hafsy se anjima nabar yara gurin kitso, gashi magriba taka kai kin rik'eni, hmmm kinga natafi, tarakata sukai sallama.

Gidan Yawa takoma, yawanci basa nan, gidan yayi shiru, tanata sauri, tawuce lungunan ganin bakowa gurin sekukan tumakai da kaji.

"Jitai an janyota had'e da toshe mata baki, kici-kicin tak'wace take amma takasa, ga ba halin ihuu an rufemata baki.
Shikuwa lalubar yadda zai yaye hijabin jikinta yake.
Ihu take tana k'arawa amma babu maijinta balle aka mata agaji, yadda aka rufe mata baki

😳Waiyo Naja'atu lovers!!

© *Aneesa_Didi*
[2/18, 10:48 AM] +234 703 962 5239: [15/11, 5:30PM Didi]
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....* ♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*35-36*

Tsam yarungumeta a jilinka, yana sauke ajiyar zuciya, Rik'o yamata bata yadda za ai tak'wace, kyakkyawan motsi kasawa tai, ambaton Allah kawai take azuciyarta yakamata d'auki.

Kici-kicin yadda zata k'wace jikinta take. Wani  k'arfi taji yazo mata, Gwiwar hannunta tasa tabugamai a fuska.

"Beyi aune ba yaji bugu a idansa, ihu yake yana k'arawa ganin haka yasata gudu bata tsaya ko ina ba sai d'akin Inna.
Kan meye wannan mutan gida duk sun firfito, ganinsa sukai rik'e da ido yanata zunduma ihu, seda yayansu Sale yazo yajanyeshi.

Kallo duk mutan falon suka bita dashi wasu daka cikin yayunta dabasu gama tafiyaba, ganin tashigo ba sallama kuma se kuka take, toilet tai saurin shigewa dankada ma su tambayeta abinda yafaru.

"Kuka take kamar an aikomata da sak'on mutuwa, ganin abin nata bana k'are bane yasa Inna tashi tabarta, hannun Innar ta rik'e tacigaba da kukan, ganin haka Innar takoma tazauna,

lallashinta takomayi hartai shiru, asannan tagayawa Innar komenene.

"Hankalinta ba k'aramin tashi yaiba, dajin abunda yafaru abinka da mahaifiya 6oye tata damuwar tai tareda lallashin, Naja'atun tayi mata nasiha mai ratsa jiki. Kwantawa takoma tayi tanata juyayin abun cikin ranta.

"Cikin kwanakin da suka biyo baya, zancen tsiyayewar Idon Saminu duk yabaza unguwa, Naja'atu kamdamuwace fall aranta, duk tabi tarame abinci ma dak'yar takeci. Ko bacci take arazane zata tashi, ganin yanayin nata yasa Inna tasa akaitamata addu'a da zamzam tanasha, hartafara dawowa nutsuwarta, niyarta takoma Islamiyya, amma ita kanta fitar baso take ba.

Zaune take tana karanta novel mai suna *'Yar Baba*tanata nishad'i abinta, k'arar wayarta taji Inna ta mik'omata, ganin Usman ne, cikin raha tace "yau antuna mu kenan"

"Hmmm yaja gauron numfashi yace "hakanema? Ke kin tunani ko saud'aya, gara nima za amin uzuri, tinda karatu yarufeni.

"To amun afuwa banji dad'i bane kwana biyu.

"Subhanallah! Miyasami ```Q```ueen of my ```H```eart? No wonder jikina yaban, kinsan yanzu kominmu d'aya. Kifito kawai kekad'ai nakesan gani, shiyasa daka dawowata ko 'yan gidan bamu ida gaisawaba nataho gurim Zuciyata.

Hmmm cike da kunya kaman yanaganinta, dukni kad'ai? Banganeba yaushe kadawo? Tace tana zaro ido alamun mamaki.

"Kifito zakigan, inba so kike nashigo cikin gidanba, kinsan nine d'angidan kekuwa haya kike.

"K'yalk'yalewa tai da daria " kai ya Usee" tunda cikin raha take yasata fad'in haka,

"Baki yaddaba kenan to natafi, dama Mama tanatamin tsiya, nazo kuma kinmin haka Nagode.

"Laaah! Afuwa DanAllah, Ina zuwa takashe wayan. Tareda mik'ewa. Band'aki tai saurin fad'awa, Inna ko tahau fad'in, " Badai wanka zakiba, mutum yayo tattaki yazo amma sekin 6atamasa lokaci.

Murmushi yai tareda shafa kwantaccen gashin bakinsa. Yasamu Bench daka gefe yazauna, kamin tafito.

Afuwa plss makaranta,
Kutaya mu addua plss Allah yabama Uncle lafiya.!!!

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:48 AM] +234 703 962 5239: {21/11, 2:00PM, Didi}
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA* ♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*37-38*

Da hanzarinta tafito daka toilet in, fuskarta fayau Hijabi kawai tasa tafita.
Tun kafin ta k'araso murmushinsa yake  mata maraba, ganin yayunta sun shigo gidan kunya kaman k'asa tabud'e tashige.

"Tasowa Usman yayi sukai Musaba ha da yayunnata. Itama tagaidasu tawuce.

"Nesa dashi tazauna bayan taimasa sallama.
"Ai nazata bazaki futo ba, yace.
"Hmm to ai kaine nasan ko zolayata kakiyi.
"Au hakane ma abun?
To yahak'uri ai gani. Fatan kazo lafiya?

"Lafia lau, Queen, nasameku lafiya, yasu Innata dakowa na family?

"Alhamdulillah kowa sunane lafiya ya,mutan gida? Ina yaya Yusra?

"Kowa Ipy tunda kika ganni, Ah tace mun kuna waya ai. Amma kink'ki yadda ku gaisa da Mama, gashi ita Sis Yusy har waya kukeyi.
"Sunkuyi dakai tayi tana wasa da abun Hijab inta. K'arfin hali kawai tai tace "to zangaidata amma ba yanzuba, nasan yanxu saika kirata" Kede wannan kunyar naki keda zaki zama matar d'anta inhmm!

"Hmm! To ai *kunya adon 'ya mace* (littafin My Feedo-Deedo). Hakane kinyi gaskiya shiyasa kike k'ara shiga raina Najata.
"Harma nazama takan? Tafad'a tana karamar dariya.

"Dariya ma kike to ai kinkusa zama, yad'an sha mur tareda fad'in "Naja'atu yau nazo da magana, dukda nasan anrigada anyi abaya, amma yanzun za akuma jaddadata.

"Ganin datai yadan sha mur seta tattara duk nutsuwatta tana sauraransa, tinda taji ya ambaci

sunanta tasan muhimmin abu zai fad'a.

"Naja'atu yakira sunanta akaro na biyu, AURE nakeso, kinga niba yaro bane, lokaci yayi tinda nakusa kammala komai gameda karatuna course in da aka turamuma miyi saura wata uku mugama. To sonake dana dawo lokacin ayi Auran, koya kikace?

"Nannauyan numfashi taja, tace "wannan maganar ai ba a hannuna takeba. Wurin manyana zaka, su zasusan abinyi.

"Nasan da haka ai, amincewarki kawai nake nema. Inkin yarda sai ak'arasa magana. Ad'aura aure kinzama tawa.

"Kasa cemasa komai tayi ta duk'ar da kanta tareda cewa "Allah yatabbatar da alkairy yashige gaba. Amma kuma.

Ameen. Amma kuma me? Kifada kinji bazan cutarda keba kome kikeso ki fad'a kunyarnan arik'a rage ta kaman ba mijinkiba yace yana darawa.

"Bawani abu bane, cigaba da karatuna kawai dama zance.

Indai dan wannanne karki damu, karatu sekince ya isheki, keda zaki aure likitan mata, kinga sekina tayani nima ko nadubaki kidubani, batare da wani yagane miki miji ko angane min mata ba.

"Dariyar da take 6oyewa saida tafito fili, wayarshi yazaro yashiga d'aukanta a hoto, bak'aramin kyau tamaiba jiyai kamar yajawota k'irjinsa koya samu sassaucin da azazzalar da zuciyarsa keyi akanta. Yai k'ura mata ido yana kallan kyakykyawar zagayayyar fuskarta. Komai kamar ita ta za6awa kanta.

Ganin abin nasa nayau yasa tace masa inyaje gida yagaida su Mama da K'annanta.

"Kawai dai kice korata kike, kingaji dani be ida rufe bakiba sega su Fawad sundawo daka Islamiyya, Salim da gudunsa yazo hannu yabashi suka gaisa, sauranma duk suka gaidashi suka wuce gida.

"Aranta taji dad'in dawowarsu, koba komai yanzu zetafi dan yau ta fuskanci da zolaya yazo mata.

Shima Usman ganin dawowarsu yatabbatar mai da lokaci yaja. Badan yasoba yai mata sallama, had'e da mik'a mata k'aramin buhun bagco daukeda Plantain, Kwakwan-manja, Kwakwa da Agushi. Mamaki tai tayi tace Haba danAllah kai kana Student hadda wani tsaraba, kaida za abama amma kaine mai kawowa? Cikin shagwa6ar data zamemata jiki hadda turo dan bakinta.(Maryam Speaker😜)

Usman kuwa galala yai yana kallanta, bak'i su dauwama a hakaba. Lallai Allah yasoshi daya had'ashi da kalan matar dayakeso, wadda komi tahad'a, "Sokike mukwana anan naga Alama,? Danai me kajika tace, toshikenan zanwa Mama waya nace 'Yarta ta rik'eni.

"Nidai baruwana ban rik'eba,  angode wannan kayan dukmu kad'ai. Allah yasaka da alkairi. kiran sallar magriba dole yasa sukai sallama, yana mai jaddada mata da kadata kashe wayanta.

"Murmushi kawai tamasa tashige gida shima yatafi.

"To bayan Sallar magriba sannan taiwa Inna bayanin kayan takarkasa tabawa kowa nasa, gudun k'ananun magana irin ta mutan gidan.

Afuwa plss makaranta.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:48 AM] +234 703 962 5239: [24/11/16, 6:22PM] Didin Anee😍
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*39-40*

Cikin watannin da suka biyo baya Soyayya sike kaman yacinyeta yakeji, dama ita kunyarsa datake matuk'ar ji yake hanata maida masa da martanin irin zafafan kalaman dayake gaya mata.
Saranar biki akai nanda sati shida.

"Cin lokacin duk tabi tarame ga ciwan Inna yatashi jikin ya matsa mata, hakan yak'ara sanyayarwa da Naja'atu jiki.

"Duk dare kafin su kwanta bacci se Innar tai amfani da wanna damar taita musu nasiha gameda rayuwa. Tak'ara had'awa da bata makamai na addu'a yadda zata bi da arun dazasu taimaketa a sabuwar rayuwar dazata shiga.

"Ba abinda takeyi se kuka dazarar Innar tafara, gani take kaman wasiyya Innar take basu.

"To ganin Innar tafara warwarewa yasa hankalin Naja'atu kwantawa tad'an fara walwala har take samun damar karanta wasu daka cikin littattafan da Innar tabata:
*ZINAREN MA'AURATA*(MY ANEE😍)
*WASIYYATUL-UMMI*
*ZAMANTAKEWAR MA'AURATA*(DIDIN-ANEE)
Dawasu sauran littattafai dasuka shafi Rayuwar Aure da Tarbiyar Yara a Musulunci. Uwa tagari kenan.

"Gyaran jiki da akema Amarya kuwa Innar ce da kanta take mata tun tana jin nauyi har tasaki jiki take gyara 'yarta duk abinda yadace takemata.
Ana cikin turareta da Dukhan Usman yabugo mata waya, gata a lullu6e badaman

d'aga wayan, dole samiha ta d'aga tasa mata a kunne, wata sassanyar dariya tasaki, meya gaya mata tace "nide baruwana a shagwa6ance, tama manta da Inna tana gurin, "mezan fad'ama to? Usman yace kina ina yanzu?

"Ina gida Allah yasa lafiya? Naja'atu tafadi.

"Yace to mekikeyi, kinmaci abinci kuwa?

"Naci mana mikagan?

"Nikam kinganni dangatan Mamata gyara miki ni take tayi. Tahad'an wani abu mai dad'i konazo nakamaki?

"La la! nids banceba baruwana. Hhhhhh

"Kinji ai ke kita kunya abundama kinkusa zama tawa, itadai shiru tamai yanatayi. Da abun ya ishetane tace ana kiranta.

Bawani kiranki da ake zaki kashen waya dai? Usman yafad'a yana murmushi abinsa. Kinga nama san komi ai da akeyi inma kin 6oyen. Sema na fad'o miki basu .......

"Ai bata yadda yakai k'arshen zancenba takashe wayan tanata murmusawa. Inna kuwa tabita da kallo tana me addu'ar Allah yasa Farincikinsu yad'ore a zaman dazasiyi.

Sunkuyar da kanta tayi ganin irin kallon da Innar kebinta dashi.

"Hada-hadar biki ta kankama, danma Amaryar tace it ba bidi'ar daza ai. Komi bisa tafarki za ayishi.

Ana saura kwana uku afara biki dangi na nesa suka fara zuwa mutan getso da Gusauma ba abarsu abayaba. Anty husna itada Ummi farin zuwa, suka cigaba da shirye,shiryen biki. Ita dai Amarya duk tak'ara sanyayewa abincima se Inna ta matsa mata takeci, setakoma dama Kunun Alkama da Madara. Dukdan kada tai rama dayawa. Bayan daffaffiyar Madarar shanu safe da yamma, tun bata iya shanyewa harta hak'ura shiyasa jikinta yai lumi, fatarta tak'ara santsi da taushi. Se shek'i take irin na Amaren da suka sha gyara.

"Ana i jibi d'aurin auren laraba dasassafe suka tafi k'unshi k'awatenta biyu Sady da Hafsa dan Nafisa a lokacin tayi nauyi. Juwairiyya Samiha harda Anty Husna suka tafi. Sun babbaje anata hira agidan lallen itakuwa seda taga anfara mata Jan lalle jikinta yakuma mutuwa ya tabbata takusa barin Inna da 'yan k'annanta jita hawaye masu d'umi sunabin kuncinta. Ganin haka itama Samiha tafara hawayen, Anty Husna kuwa mezatai inba dariyaba.

Tahau yimada fad'an ai Aure shine DARAJAR MACE. Kumashi Katangane babu wani mahaluk'i dazai kamiki wargi matuk'ar girman nan ya hauki, Rigar mutunci tamiki lullu6i duk inda kika samu kanki za abaki girma da MARTABARKI(Ummi-Aishha) ta D'IYA MACE(Khadija Sidi). Taita mata ita kuwa tak'ara rushewa da kuka. Sauran kuwa sukai ta tsokanarta. " ```Ke kikacw kinaso Amarya dabaki so da ba abaki shiba``` sukaitayi suna dariya.

"Meyi mata k'unshi kuwa dakatawa tai, tanata ganin ikon Allah. Wannan shagwa6a ta Amarya har ina.lalla6ata sukai tai shiru akagama mata lallen sannan suma akayiyyi musu.

"Bayan la'asar suka dawo mutane dayawa sun zazzo anata aikace-aikace, shigowarsu tasa aka kaure da hayaniya masu gud'a nayi abokanan wasanta suna tsokananta, kowa da abinda zaice aikuwa meneman kuka anjefishi da kashin awaki(inji hausawa) aikuwa tasa kuka. Seda wata k'anwar Babansu tazo tajanyeta, suka k'yeleta.

"Alhamis akaimata kamu irin na Al'ada, dayamma kuwa Walima akashirya Matan aure zallah se Ango da abokanansa. Kuzo kutayani ganin Amarya cikin shiga ta alfarma wata had'dd'iyar gown ce ajikinta gold colour da veil inta and'ora shi akan Top Knot inda akaimata jikinta rufe ruff light make-up aka mata ba k'aramin kyau taiba.

Malam Auwal Muhamnad da Malam Nazifi sunyi fad'akarwa sosai akan Aure. Da matakan daza subi subi su mallake junansu. Ba Boka ba Malam musamman ga ita Amarya da sauran mata. Walima cikim tsari ba hayaniya akai lectures sosai kan Addini. Kafin magriba akai addu'o i da neman Albarka acikin Auren. Akatashi itade Amarya Murmushi kawai take.

Sunda gida taga se had'a mata kayanta ake jikinta yak'ara mutuwa kamar anzare mata laka.

Ranar jumu'a Takama 24 ga watan 10 dubban jama'a suka shaida d'aurin Auren *USMAN BELLO GALADIMA* da Matarshi *NAJA'ATU ABDUL-MU'IZ AUWAL* bayan Sallar Jumu'a bisa rangwamen sadaki.

"Yinin biki aka zarce dayi bayan angwaye sunzo gaisuwar dangi akayiyyi hotuna. Amarya masha Allah kamar kasace ka gudu. Nikaina Didi ba k'aramin burgeni Amarya dashi kansa bikin yaiba. Lek'e nake tayi chan na hango su Haleema da Maman Ansar ansha anko. Sukuwa su Ukty yadda zasu Amshi take away suke. Nakallesu nace daga Take kuma se Away mukasa dariya dukanmu.

"Kuka take kaman ranta zai fice, anata shiryata wankanma dak'yar tayi.wankan turaruka Anty Husna da yar Babansu suka mata nakaima dabanne Aka nad'eta da yalwataccen Mayafi, gurin Babansu aka kaita yaimata iya tashi Nasihar yahad'a mata da Al-Qur'an charbi da babbar Dadduma, shima jiyake kaman yasa kukan.

Zagayawa da ita akai gurin sauran matan gidan suma sukasa Albarkacin bakinsu. Masu yada maganganu nayi kowa da abinda yadameshi.

"Itadai Inna k'arfin hali kawai take, "Allah yasa kishiga a sa'a abinda ta iya furtawa kenan. Tai musu alamada hannu aka wuce da Amarya. Deedat ya k'ank'ameta shi bazata tafi tabashahiba dayawa cikin mutan gurin saida sukai k'walla. Aka tafi da Amarya gidanta dake Sharad'a. Gidan ya k'ayatar da mutane danba k'aramin dukiya dangi suka narka mataba. Kowa yataho akabar ta daga ita sai halinta.

Semuce Allah ka d'anbaba mai k'uli-k'uli😜

Am so sry makaranta Abubuwan dayawa shiyasa baku ganin postn akai2. Inkomi ya gyaru zakunajina koda yaushe inasanku nima aduk inda kuke. Allah bar zuminci da k'aunar juna
Luv u all😘

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:48 AM] +234 703 962 5239: [25/11, 2:50PM] Didin Anee😍
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*41-45*

Abokanan Ango sukayo masa rakiya suka wuce bayan sunyi Addu'o i danemanmusu farinciki dazama lafiya mai d'orewa. Suka d'anyi ciye-ciyensu itadai akunyace tasha Ruwa shima danya matsamata ne.
Usman ya Umarci Naja'atu data sake alwala, cikin toilet in d'akin tai Alwala. Sallar isha suka fara sannan suka d'ora da nafila yai musu Addu'a mai tsaho sannan yai mata tambayoyi gameda Addini, yak'ara mata haske har Wankan Janaba yakuma mata bayani dayadda take samuwa. Kanta a sunkuye yake tamata bayani, wani tai magana wani tai shiru.

"Hannunta duka yakama, yajanyota jikinshi janye mayafin duka yayi yarungumeta tsam ajikinsa, dukda hakan bak'on abune agurinta jinta tai she is safe, zippin rigarta yasoma yana kuma cusa kanshi ajikinta cikin wani salo na soyayya dabata ta6a tunanin haka abin yakeba, nikam danaga lamarin yajuye abin yafi k'arfin ganina. Najuya nabasu guri.
Kunsandai bakyau bincike balle su wannan daya zama sirrinsu. Asuba tagari couples.

"Wayewar asabar, komi shiyayi mata, Addu'a kuwa tashata ba adadi takuma narkewa soyayya yake gwada mata wadda ba algus acikinta. Har sukai karin kumallan safe. nok'ewar da takene adan fusace yace "ai aikin gama yagama, abunda take kunyanma yagani tomiyai saura? Itadai murmushi kawai take tana k'ara sunkuyar dakai. Kujerar da take kai yadawo ganin ta mik'e yasashi janyota tafad'a kanshi. K'ok'arin zamewa take yak'ara k'ankamota.
Zauna ma kiji abinda zaki fara ma shine indai ina gida bakida gurin zama daya wuce nan, yanuna mata jikinshi. Kinsan body contact yanada tasiri wurin shak'uwa da mararin juna ga ma'aurata.

"Bugun k'ofar da akeyine yadakatar dasu, saurin mik'ewa tai daka jikinshi tayafa mayafi akan kayanta tanufi k'ofa danta bud'e, Abdullah ne da Shukra k'annan Usman mama ta aiko suka

mata abincin Rana.
Guri tabasu suka shiga falon gaisar da Yayan nasu sukai, itama suka gaidata tacikasu da kayan mak'ulashe. Shukra Autar mama dasaurin sabo duk inda Najan tayi tana biye da ita. Har Usman ke tsokanarta tayi 'yar zaman d'aki, murmushi tai tace " aikam danaji dad'i daza abarta ta zauna.
Hararar wasa yabita da ita tareda fad'in "bakowa ma kink'i sakin jiki musha Luv inmu bare anka miki wannan mai surutun. Tace " aida Mama zata ban ita danaji dad'i.

"Hmm! Bakisan yadda Mama da Shukra suke bane bame rabasu se makarantar data shiga amma da ko ina suna tare, har yanzunma. Bata yadda tazauna agidan kowa se Mama. Dakwai sanda mama suka tafi Dabinai aka kaisu gidan Sisto, har yamma basu dawoba data fara kuka, kowa seda yaji haushinta Sadiq da Anas sukai zamansu harsun kwanta amma Shukra seda akada da ita gida k'arfe 10 nadare. Tana ganin Mama shiru kikeji.
Wai lallai kuwa naga ranar rabuwarsu da Mama. Allah sarki aikam dolene rabuwar ta fad'a tana rau-rau da ido.
Laah! Nibance kiman kuka ba kingama natafi. Yafice daka kitchen in yana dariya.

"Bak'i sukai tayi danginsa da nata danma ankakkamata abinci taita zuba musu faranfaran takar6i jama'ar. Tacikasu da kayan arziki.
Washe garima haka sauran danginsu dabasu tafiba sukazo ganin idan amarya.

"Anty Husna dasu Samiha se yamma suka tafi bayan sun gyaramata ko ina dasauran kayayyakin ta nagida, takuma ware wasu kayayyakin daza a rarraba harda wasu daka cikin kayan lefanta. suka turare mata gidan bayan anty Husna tasata tai wanka kwalliya sosai tasa tayi, dan yanzu bada bace dole sekina gyara ladabi da biyayya sannan zaki mallake mijinki atafin hannunki. Kud'an bamu guri tace dasu Samiha. Suka fita suna k'us-k'us batasan yaran zamani wasu sunmafi masu Auren sanin abubuwa ba.
Tacigaba dabata tip da dabarun zama da miji. Da sirrikan dazasu k'aramata Ni'ima batareda tayi amfani da abunda zasu cutarda itaba wanda batasan dame akaiba.

" *Sirrri na daya*:- kisamu kankana kiyayyanka kisa madara kinasha.

" *Sirri na biyu*:- kisamu zogale ganyansa da cocomber kiyi blending insu sekisa zuma da madara zakisha mamaki.

" *Sirri na uku*:- kwakwa dabino dankalin,hausa(kadan) farar shinkafa cukwi. Ki markada shiima kinashan ruwan. Inkinso kuma zaki iyayin na gari kina damawa da madara kinasha.

" *Sirri na Hudu*:-kihadasu gero mazankwaila dabino farar shinkafa kwakwa busasshiya busasshen muruci kida kasu siyi gari. Seki zuba man habbatussauda kihadesu guri daya. Yazama gumba.

" *Sirri na biyar*:-Man zaitun Man tafarnuwa Man Habbatussauda Miski kihadesu kina

shafawa/insert.har maganin sanyi yikeyi.

"Taita gayamata abubuwa tana rubutawa wanima intayi harshi zasuna sha kaman inzata dafa shayi tazuba Minannas da kirfa aciki kunasha tare tsafta dayadda zata tsaftace gida da jikinta turaren bayan kunne daban nagashi, na matse-matsi cibiya. Shikansa mijin tadinga tsaftaceshi da kayansa yadda bazai taba zamada daud'a ba balle ajiwani unwanted odour yana tashi daga jikinsu.
Seda Anty Husna tacikata da abubuwan Alheri sannan suka tafi tanata kewarsu.

"Alwala tai tazauna kan akira sallah tanata lazimi abinta. Alamun bud'a k'ofa taji da sallama yashigo cikin husky voice insa, sansanyan k'amshin turare yaji yabigi hancinsa wanda bazai tantance ainayi wasu iri bane. Tun alokacin tafara aiki da hud'bobin Anty Husna.
Tasowa tai zuwa inda yake ganin kaya da ledoji fal a hannunsa tarusuna tamai sannu da zuwa takar6i kayan hannunsa janyota jikinsa yai yakuma jin wani k'amshi na musamman natashi. Eye ball to Eye ball suke kallan junansu yana mata wani sassanyan kallo da murmushi dashi kad'ai yasan ma'anarsu.

"Kinyi kyau yace da ita. Tallafota tai tagefansa suka k'arasa cikin falon, takai kayan inda yadace shikuma yai Alwala yatafi Masallaci.

"Cikin kwanakin Amarcinsu kawai sukeyi, seda tai sati sannan yakaita gidansu tagaida Mama da Abbansu. Dabinai kuma seta k'ara kwana biyu zaikaita taga danginsu nacan. Yanata rawar kai agaban Maman itakuma duk yasa tatakure, Maman bata k'ara ganin rashin kunyaba saida suka gama abinci tazubamai waishi da Matarsa zaici. Taitamai tsiya kuwa, itadai Naja sai murmushi kawai take ta duk'ar sa kanta. Da Maman tagaji da shak'iyancin nasa tace itama tatafi gano nata Mijin. Bak'aramin burgeta sukaiba yadda suke abunsu faran-faran kamar ba Mahaifiyarshiba. Komansu a kammale ba raini  in social life. Taji sunk'ara shiga ranta. Musamman mijinnata. Habeeb  injita da fad'a dukdan karta ambaci sunanshi. Yayi-yayi da ita amma taki, irin abubuwan dasuke k'aramata Martaba da Daraja agurinsa Allah yai yawa dasu, banda zazzafar Soyayyar dayake mata wadda bazata misaltuba. Agidan suka wuni se dare sannan suka tafi tinda bawani nisa garesuba duk Unguwa d'aya ce.

Kubiyo *Didin anee*😘 danjin ya rayuwar Naja'atu  zata kasance bayan Aurenta???

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:49 AM] +234 703 962 5239: Didin_Anee😍
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*46-50*

Da k'afa suka k'arasa gidan, shi yabud'e musu get in gidan tunda ba maigadi garesuba. Seda yakunna hasken gidan, Masallaci ya wuce dangabatar da Sallar Isha, ita kuma tashiga ciki, wanka tafarayi tagabatar da tata sallar, shafa tazaunayi rigar bacci tasa silk light blue, turare tafeshe jikinta dashi, kowana sak'o seda ta mulkeshi da nashi kalan turaren. Tahad'e gashin kanta da ribbon tareda d'ora hula aka. Jin shiru beshigoba yasata dawowa falon kallo takunna, Eternal Love take kalla a Ztv.

Bata dad'e da zamaba taji Karan rufe k'ofa Alamun yadawo kenan, da d'an saurinta tataroshi, kayan hannunsa ta kar6a tai kitchen, tana wawwarewa yashigo kitchen in. Yatayata aje kowane abu agurinsa ita kuma tayayyanka fruits in dayashigo dashi, tin a kitchen in yahau shan kankanar datake yankawa, dataga haka ta d'auke plate in kankanar ta ajemai na lemo dasauran kayan fruits in.
"Abun ma hakane? Yafad'a ashagwa6e kaman shine matar, ganin tayi blending in ragowar Kankanar, ido kawai yabita dashi tamarkad' kankanar tasa madara da zuma amemakon Sugar. A fridge tasa tagyara gurin suka fito atare daka kitchen in se murmusawa take ai kuwa ya hau fad'in.
"Shifa beyadda da wannan murmushin da take ba, tafad'a masa metake shiryawa.
Murmushin takumayi sannan tace "bakom muje nahad'ama ruwan wanka tinda ba abinci zamuciba. Tashige cikin d'akin tana dariya ganin yadda yabita da idanu kaman baisantaba.

"Ruwan wanka ta had'a masa wankanma seda ta lalla6ashi yashiga. Wai yayi fushi tinda tak'i gayamasa metake shiryawa. Kayan bacci tafito mai dashi tafeshesu da turare, tak'ara kintsa d'akin dukda bawani datti yaiba se bada k'amshin freshner yake.
Kallonta tacigaba dayi tanata farin ciki itama da Allah yabata miji irin Usman. Ganin yadda Sahiba da Ranveer suke zuba salon tasu soyayyan.

"Kitchen tashiga, ta d'auko kankanar datai blending tayi sanyi, bame yawaba tazauna tanasha, d'an sanyi dayai yanabin jikinta harwani lumshe ido take, k'anshin turarensa kawai taji tabud'e manyan idanunta duka akansa, k'arasowa kujerar datake yayi yazauna jikinsa na gogar nata. D'ebowa tai zata kai bakinta yai saurin kai nasa bakin, "irin dad'in dakike sha kenan ashe, yafad'a yana lumshe narkakkun idanunsa.
Sunkuyar dakai kawai tai murmushin de takuma, hannu yasa ya d'ago fuskar yahad'ata da tashi kowa nashak'ar numfashin d'an uwansa, yana mata wani sassanyan kallo dashi kad'ai yasan ma'anarsa. Cup in hannunta ya kar6a yana bata yanasha har suka shanye, seda yakalli News sukai brush yasunkuceta sukai d'akinsu. Tareda rufo k'ofa.
Safiyar alkairi.

"Kwance yake kaman bazai tashiba tinda yai bacci dagari yafara haske, bayan yagama yamutsa Naja atun Queen injishi da fad'a.
Wayan tak'ara ringin akaro na uku, jin vivration in yayi yawa yasashi bud'a ido da kyar.

Ganin a sch inda sukai ne yai saurin ansa wayar, "ok godiya nake prop, Allah yak'ara girma. Yamike yashiga band'aki already yasan tahad'a masa ruwan wanka ilai kuwa tarufe mai ruwan yasamu yayi daidai wanka.

Wajen k'arfe goma yafuto, se kamshi gidan yake, yaduba ko ina batanan yai d'akinta.
Sark'a take k'okarin sanyawa, ya kar6a yasa mata har d'ankunnen yak'arasa shiryata, tana tabinsa da kallo ire-iren abubuwannan dayake mata nakulawa da soyayya su suk'e k'ara mata k'aimi wajen yin duk wani abu datasan zai farantamai yasashi nishad'i da farinciki cikin d'an zaman dasukayi tare. So da K'aunarsa kuwa sun mamaye jini da jijiyoyinta, duk wani motsi da zatai da k'aunarsa take, Addu'arta kullum suzama cikin so da k'aunar junansu da farinciki mai yawa a rayuwarsu.

"Rungumeta yai tabaya yad'ora ha6arshi a kafad'arta, suna kallon junansu ta madubin.
"Queen Tunanin mekike kina tare dani? Idan muna tare bakida sauran damuwa a rayuwanki. Am always there for you. *Ina tare dake*(Meemee bea ta) cikin kowana yanayi *Komai Rintsi*(Hama Gee). Kikasace dani kowana hali samu da rashi, cuta da lafiya yafad'a yana k'ara rungumota kaman za a k'wace masa ita.

"Hannayenta duka tasa tana shafo kansa, tahau rattabomai tsadaddun kalamai "kazama ni nazama kai mijina komai inzanyi dole saidakai. A kullum ina godiya ga Allah daya bani kai mai hak'uri da kawaici mijina takuma narkewa ajikinsa. Sund'au lokaci suna kallan junansu kowa na Sakar zuci sukasa dariya gaba d'ayansu yabata kiss a fore head inta, dak'yar yabari ta d'aura d'ankwalin suka fito dansuyi break fast.
Agurguje yaci abincin, shima saida tai kaman zata masa kuka yazauna dakanta tabashi Oat ne yaji madara da Omylet, tanad'e mai Pan cake a foil da ginger drink aroba yatafi dasu. Dan idan yai irin fitar wurinnan baya dawowa da wuri, takanyi k'ok'arin yimai dabarun dabazai sa yaji yunwa dawuriba. Tinda ba abincin ko ina yake ciba.

"A ranar ma kuwa se yamma yada gidan. Tana zaune itakad'ai se Radio data kunna, wak'an Nayi gamo ake tana tabin wak'ar dan tana santa(Miss zo6o😜) kawai ganin mutum tai jitai anyi sama da ita tai saurin rintse ido, yai juyi sosai sannan ya ajeta. Neman kujera tai tai saurin zama gudun fad'uwa, seda ta maida numfashi ta iya cemai sannu da zuwa, kusada k'afarta yazauna yana "Addu'ar dakuke min a kullum ta k'ar6u anza6eni cikin wanda akai sponsoring inmu miyi masters a sch in damuka baro, dan haka kihau shiri dake za atafi. Dirowa kansa tai tarungumeshi tanata murna itama, jin bakinsa tai cikin nata tin tana tirjewa harta soma maidamai da martani ganin yana neman zarcewa yasata janye jikinta tai gefe sunata ajiye nannauyan numfashi.

"Ruwa takamai yasha suk'a k'arasa maganar nanda wata biyu zasu tafi, kannan itama zata zaga dangi har gida zata tinda yau wata4 da zuwanta gidan bataje gidaba. Shiko yajajje gaidasu. Kafin magriba yatafi gida yagayawa Mamansu da Abbansu. Suji zancen suma. Sula kuwa samai Albarka dafatan samun Nasara arayuwarsu gaba d'aya.

*Bayan Wata biyu*

"Kafin lokacin seda tazazzaga dangi, dasukaje gida kuwa Inna kamar tacinyeta dan farin ciki ganin yadda 'yarta takuma cika da murjewa fata se shek'i take alamun hutu da kwanciyar hankali. Tawuni cir agida har mak'ota tazazzagaya.
Gidan Yayarsa Yusra ma takar6esu hannu biyu-biyu sukai ta hira kamar sun saba. Tahado mata abubuwa dangin kayan k'amshi tinda su take siyarwa.

"Daga getso suka ziyarci dangin mahaifinta, yacikasu da shatara ta arzik'i wanda basu sanshibama duk suka ganshi. Gusau suka wuce kwanansu biyu Anty husna kam tafi kowa farin cikin zuwansu. Tak'ara mata dabaru da sirrika irin na Mata masu aji.

"Seda sukai kwana biyar dadawowa daga Gusau sukai shirin tafiya Dabinai. Suka k'ara kwanaki acan yadda dasunda se shirin tafiya. Taga karamci da mutuntaka irinnasu, taita godewa Allah daya had'ata da miji da danginsa masu so da k'aunarta da mutuntata. Tsaraba iri daban2 suka had'o su dashi taita kunya ganin ita bawani abun azo agani takai musuba. Turaruka sai k'ananun turamen atamfofi takai aka rarraba. Sukai ta farinciki dasa Albarka.

"Tun ana sauran kwana5 sutafi kayansu sukai gaba a motar haya, se d'an abunda ba a rasaba, sunata shirin tafiya. Agidansu Usman ne Mama taita musu Nasiha musamman ma shi tinda ita bak'on guri zata shi bayau yafara zuwaba. Tajamai kunne yarik'e mata 'yarta Amana. Yaita dariya yana "ya kar6a to shi wazai rik'eshi? Allah mana inji Maman sukaita abunsu. Itadai Naja kanta a sunkuye. Tana k'ara san sirikar tata da irin d'abi'unta.

"Dayawa daga cikin dangi sunmusu rakiya, haka sauran likitocin da aka za6esu suma yawanci 'yan uwa sun musu rakiya. Akaita sallama da 'yan uwa da abokan arzuk'a. Se alokacin jikinta yai sanyi. Dan tasam zatai kewar gida da dangi gaba d'aya. Taita Addu'ar Allah yahad'ata da abokan zama nagari. Hawaye kawai yagani a fuskarta. Yasa handkchf yasharemata tareda kamo hannunta suka shiga jirgi, tak'ara narkewa ajikinshi tana kewar ahalinsu.

Kowa yabar gida.... Gida yabarshi inji hausa people..!!

Semuce asauka lafiya!
Team Naja'atu suna rakiya..😜

Am realy sory makaranta. Zaku naji yanzu in sha Allah akai akai. Tnx 4 ur luv and prays. Luv u all😍😘

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜

[2/18, 10:49 AM] +234 703 962 5239: {5/12, 9:35AM} Didin_Anee😍
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*51-55*

``` EDO STATE```

Saukarsu keda wuya babbar mota lexirius ta makarantar ita tazo d'aukansu, takwashesu dukansu masu mata da singles in d'alibai.

To tun amota Naja'atu ta lura da wani abokin karatun su Usman d'in ya kafeta da ido duk wani motsin dazatai a idansa yake koya ta d'ago ido sesun had'a ido dashi. Har aka saukesu a Staff Quaters, yawancin masu Aure 2 room apartment aka basu, sukuma marasa matan wasu suna Hostel wasu kuma su 4 gida d'aya aka basu.

"Gida ne matsakaici, babban falone da toilet ahad'e mai d'auke da d'akunan bacci kowanne da band'aki aciki, kitchen matsakaici se varenda.

Tinda suka sauka agidan ruwa kawai ta iya sha suka hau gyara ko ina, sauran kayansu ta aje kowanne a inda yadace. Ruwan wanka tahad'a masa yayi, itama tashiga tai.

"Ranar dai bai barta tayi girkiba. Darana abubuwan dasuka taho dashi sukaci da yammaci kuma yayo musu take away.

"Rayuwarsu a garin tai musu dad'i, rayuwa suke cike da so da kulawa ga junansu. Baya ta6ayin nesa da ita saidai in makaranta yashiga ko Teaching Hospital in da aka turasu. Dayawa mak'otan datayi ba hausawa bane, ita da Fatima matar abokin Usman d'ince sune kad'ai Hausawa itama ganin yadda Fatyn take fiffik'a da d'aga kai yasa tarage shiga sabgarta. Yawanci in yafuta gidan Maman Benue take shiga sita hirarsu takoyamata abubuwa dayawa irin na yaransu da abincikansu. Ba bak'inciki ko hassada zama suke na amana da mutunta juna. Kafin itama yanemarmata gurbi ta d'ora karatunta a Jami'ar tasu. Matsalarta guda ta wani abokin karatunsa maisuna Salis amma amfi kiransa da Baby. Yadda ko kallanta yakeyi seyai wani k'asa da idanu kamar d'an maye.

"Sallar walha ta idar tanata addu'a yau batajin fitar ma, bugun k'ofa take taji, tinaninta Usman ne to amma in shine a yanada key bud'ewa kawai zai inya k'wank'wasa sau d'aya, bata cire hijabin jilkinta tai hanyar k'ofar ko mak'otane. Salis(Baby) tagani yabita da Shu'umin kallansa, yace "Minyi waya da Usee in yanzu zai dawo yace najirashi"

Jin haka yasa tabashi hanya yawuce, kamar wani gidansa yazauna a inda suke zama tareda d'ora k'afa d'aya kan d'aya yana chanja tasoshi, sa6anin da datakai saudi Qur'an tana
```

sauraran K'ira'a, tinda taji yace Habibintane yace yajira shi, kitchen tashiga takamai dambun naman datai jiya tahad'o da lemu, ruwa da cup a tray. Ganin ta ajemai yasakar mata murmushi tareda cewa "godiya nake  Sarauniya. Itadai jitai wani banbarakwai wai sarauniya. Saurin d'auke tunanin maganar tai aranta.

"Tin wajen 11:30 yazo gidan, tanata 'yan aikace-aikacenta, dukda a d'ar-d'ar take dan basan zamansa takeba. Kitchen ta shiga ta d'ora girki Tuwan Semovita tai da Miyan Kuka tabirge kaza aciki, tuwan kuwa ta mulmuleshi a leda tasa a warmers. Kafin biyu ta kammala tashiga wanka. Ta had'o da alwala seda tashirya cikin riga da skirt na atamfa tai sallah, tana cikin d'aura dankwali taji sallamarshi, kafin tafito har Usman ya shiga toilet, tai sauri ta kammala kintsawa cikin sassauk'ar kwalliyarta tad'ora babban mayafi akan kayan.

Kafin yafito tafito mai da k'ananun kayan dazai chanja. Tak'ara tattare d'akin tai kitchen.

"Babbar leda da ake cin abinci akai ta shimfid'a tajere wermers guda biyu na Tuwo dana Miya ga roban manshanu da yajin daudawa agefe, tasamusu plates masu zirfi biyu da cokula ga roban wanke hannu agefe komi dazasu buk'ata ta ajiye. Usman Yana fitowa kuwa suka hau cin abinci. Salis(Baby) yanata zuba surutu Usman sede yai murmushi ko "Ah, A'A" danba d'abi'arshi ceba magana inyana cin abinci. Naja'atu tana gefe taji yak'ara bata haushi kaman ta bubbugeshi kawai sotake yatafi amma ba alama.

A kwanakin da suka biyo baya Salis(Baby) yamaida gidan gurin zuwansa inbezo daranaba zezo da dare tinda dasafe suna asibiti ko makaranta. Ko Usman d'in nanan kobayanan haka zaizo. Yabi yashiga jikin Usman sose komai tare suke. Abun yafara damunta tarasa yazatai da lamari irinnasa. Rufe k'ofa tafarayi, koyazo tanaji bazata bud'eba, hakan kuwa ba k'aramin rigima yasa sukayiba. Ranar tasha mamakin Usman din akan wani aboki zenemi yatada musu da hankali. Yak'ara jaddada mata indai yazo ta bud'e masa ai arzik'i nema anuna anayi dakai.

'Yar rama tafara dalilin sa damuwa datai aranta. Ganin zata jawa kanta ciwo yasata cire komai  daka ranta ta fauwalawa Allah lamuranta da duk wata damuwarta. Allah yabayyana gaskiya kowa yaganta.

"Fuskarta d'auke da farin ciki tagama waya da Mamansu Usman takira Innarsu, bayan sun gaisa take sanarmata da kud'in auren su Samiha za a kawo, dan babansu yace duk aure zai musu kowacce tacigaba da karatunta a d'akin mijinta, murna kaman tarufe ido taganta agaban Innar tasa albarka suka gaggaisa da 'yan k'annanta tai hanging wayan.

Gama wayanta keda wuya Maman Benua tashigo. Ganinta yasata fad'in "kinji shiru ko mama(wani lokacin haka take kiranta tunda tagirmemata) kika biyo bayana, ainace nadena zuwa tunda bakyasan shigowa. Maman benua kuwa cikin rikitacciyar hausarta tace "baniso nazo mijinka yadawo yaganni nahanaku sakewa bare masoya irinku "to mezaimiki kai Mama made yanzude mekika kamun? Sukai tahira abunsu secan tatafi nata 6angaren.

*Six Month letter*

Seda sukai rabin shekara sukaje ganin gida, Naja semunna take dantayi kewarsu bakad'anba.
Nagaya miki ba inda zaki ga gidanki shima yana buk'atarki, kawai de ko ina kyaje ki wunan musu. Turo baki tai had'e da muryar shagwa6a tana "haba nawan dan Allah ko kwana biyu kabarni nayi yaushe rabona dasu.
Nafa gama magana nagaya miki yaja bargo yakwanta. Itama kwantawa tai tajuya baya sa6anin da dasetajita manne ajikinshi suke bacci, sabo dolenta tajingina dashi tahau baccin.

"Duk inda yadace seda sukaje, cikin sati biyu damin sati uku zasiyi, duk tabi takasa gane kanta, barin hakan tai dalilin zaman dabasayi.
Randa taje gidansu kuwa Inna duk tagano komai dake tattare da 'yartata, tak'ara cika da murjewa abin gwanin birgewa taita k'ara addu'a aranta. Naja kuwa sawatai akai mata d'anbagalaje taitaci kamar an aikota. tofi azam-zam innar taimata tasha, haka taitayi tana aikamata kansutafi.
Dazasu koma kuwa taimata tofin dayawa tahad'a mata da kayan kad'i yaji K'uli-k'uli har garin rogo seda tahad'a mata. Amota kuwa warin fetur yahau kanta taita kwara amai. Agalabaice dai suka dawo seda ya d'aura mata drip tada hayyacinta.

"Wani abu data futo dashi kuma cin k'uli-k'uli, taitace wataranma hadda lemu take had'awa. Idantasa daru dolensa yanemo ko a inane, ganin haka yasashi d'aukar jininta yaje lab in cikin sch dashi bayan yayi Spinig in Blood in yai Pragnency test, anan yaga positive result. Godiya ga Allah yafarayi, no wonder abubuwan da Queen keyi kaman shigan ciki ashe shid'inne. Lallai ubangiji yanasanshi tinda yaza6eshi cikin wan'yanda zasiga k'wansu a duniya. Yak'ara godewa Allah. Jiyai soyayyar Naja'atu da abinda ke cikinta tunkanma yaga meza a haifa tak'aru. Bejira komaiba yakoma gida.

"Tana tsaye tana gugan inner wears insa, jitai an d'agata juuu anjuyata, abinka dame jiri jitai tana neman fad'uwa, saurin tarota yai a jikinsh taruntse ido tareda k'ara k'ankameshi tanasake saka kanta ajikinsa.

"Kujera ya ajiyeta, yasamo ruwa yabata tasha.seda ta da nutsuwarta yatambayeta meke damunta?
"Itadai ba abinda kedamunta se nauyin da jikinta yayi, kuma taita kwad'ayi wasu lokatan, tace tana yamutse fuska.

"Lakuce mata hanci yai yace to k'aruwa muka samu. Babynane acikinki shike saki komi kikeji.
Aibata bari yak'arasaba ta sadda kanta jikinshi cike da kunya. Add'ua yaita mata yana gaggayamata abubuwan dazata kiyaye da irin wanda zatana ci. Sekuma zuwa asibiti yakuma dubata acan.

"Naja'atu tak'ara kyau takuma murjewa abinka dame matashin ciki.
Zaune take tanacin Teba da miyar Ogun da Maman Benua taka mata. Tanaci d'an tsamin teban namata dad'i, har wani lumshe idanu take. Daka ita sai wando three quater iya gwiya yamatseta da 'yar ficilar rigarta me fad'i cikinta d'an wata hud'u yataso sosai kaman wata

takwas. Jitai kawai anbud'e k'ofan, tajuya ma k'ofan baya.  Tasande bame shigowa se Usman, maidakai tai tacigaba dacin abincinta.

Hannu kawai taga ansaka a kwanon. Yadda kuwa takeji dad'in abincin kowaye bazata bashi yaciba. Janye kwanan tayi tace gaskiya Habeeb bazakaciba a shagwa6ance tai maganar.
Haba Sarauniya nid'in?
Jin haka yasata dubansa dan bahaka yasaba gayamata ba.

"Caraf idanunta cikin nashi, Innalillahi kawai tahau ambata cikin razani tanemi tashi amma takasa dan suman zaune tayi...

Nima zaro idanu nai👀 nai duba garesu duka!!!

Kubiyo didi. Danjin yazata kaya!

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:49 AM] +234 703 962 5239: {12/12, 5:00PM} Didin Anee😍
♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*56-60*

Zafafan hawaye taji suna bin kuncinta,  ita tarasa wannan wace irin rayuwa ce sam mutum baida sakewa acikin gidan, kawai wani k'ato  yashigo batare da ambashi iziniba, kome gidan aiyana nuna alamun dawowarshi bare wani daban.

Tana daka zaune take jada baya, ganin haka yasashi mik'ewa.
Batasan sanda tafara gaya masa maganganu marasa dad'i ba. Ta inda tashiga batanan take fita ba. Tanayi tana kuka. Fita kawai yayi batareda yace komaiba.

Ranar kasa gane kanta Usman yayi, daya matsa mata da magana tasa mai kuka, badan yasoba ya hak'ura da tambayarta yajanyota jikinsa yana shafar bayanta.

To cikin kwanakin sam yakasa fahimtarta, abincima dak'yar takeci duk tabi ta ruruce masa banda ramar datayi se tulin ciki datake fama dashi fuskarta tai fayau. Hawaye kawai taga yanabin kuncinsa ad'an firgice ta d'ago tana kallansa, yahau fad'in "Queen yakikeso nayi? Nayi nayi kifad'amin damuwarki kink'ki, ko gida kikeso namaidaki?
"Ah ah" tace tana girgiza kai "to mikikeso kowani abun namiki plss Queen kifad'amin. Banasan duk wani abu dazai takura rayuwarki akullum banida addu'ar data wuce murayu cikin aminci da k'aunar junanmu da tattali har tudun tsira. Yaita gayamata kalamai masu shigarai da kwantar da hankali.

Hawaye tashare yabata tausayi bakad'anba, tashiga yimasa bayani duk irin abubuwan da Salis(Baby) yake mata tun randa suka zo garin har k'arshen zuwansa gidan. Yadad'e yana jimamin abun idanunsa sukai jajir yana fidda wani gauran numfashi, ya hasala sosai, ganin yai haka tashiga bashi baki. Har zuciyarsa ta sauka. Abinka da mata da miji sai Allah (Maganar gaskiyace) suka shirya kansu kamar ba abinda yadamesu.

Washegari tun safe yatafi da ita asibitinsu. Inda yake kaita  Antinatal. Sabida complain in datai na nauyin jikin datakeji dole aka mata Scanning. Murmushi kawai yake dayaga hoton 'ya'ya kwance acikin mahaifarta dakoni Didi bebarni nagano muku guda nawa bane. yaita tasbihi da godiya ga Allah. Ranar kaman yamaidata ciki. Ko suraba cikin yakeji. Seda yakaita gida danufin zeda dayamma sud'an zagaya. Tana shiga kayan jikinta tarage ta watsa ruwa tazauna daka ita sawata riga iya gwiwa me fad'i. Bacci tahauyi harseda yunwa tatasheta. Sallah tai tashiga kitchen.

Tana tsaka da jajjaga attaruhu yashigo gidan, kai tsaye yayo kitchen in jin k'amshi yacika gidan. Da sallamarsa yace "Queen mikike dafama unborn babys ina kuma?
" Babys kuma? Tafad'a tana kallansa.
Bagarar da zancen yayi yahau bud'e tukunya.
Karka k'one Habibi Taliya nake dafawa me daudawa, murmushi yayi baice komaiba yak'arasa mata jajjagen yayankamata albasa harta kammala suka gyara gurun. D'aki yanufa dan yawatsa ruwa. Itakuwa kafin yafito tabaje ak'asan carfet tahaucin abincin kaman tashige kwanon.
Futowa yai kawaiy gani yai tanata zuba loma duk ta had'a zufa, fanka yayo saitinta da ita yazauna tareda nad'e k'afafu, sa6anin itada ta ware k'afafu cokali yagani agefe dawani plate in. Bismillah yayi yahaucin abincin adaddafe yai spoon biyar yakur6i lemon dake gefe. Ita kuwa seda taji dam cikinta ya d'auka taja gefe, kallanta yake kawai cike da tausayi dan duk tafara kunbura tunkamin cikin yatsufa ma kenan inaga yatsufa. Dakansa yad'auke kwanunkan yamaida kitchen. Yazauna sukaita hira abunsu.

Wajajen bayan la'asar suka fita, sun d'anyi nisa damakarantar ganin tafara gajiya yasamammusu taxi. Kasuwa yakaita taga abubuwa iri-iri na al'adun yaroba da Igbo awani 6angaren kuma hausawa ne. Siyayya yamata sosai mother care haka kayan baby komai setaga ba guda yad'aukaba itadai binsa kawai take ta idanu inya d'au wani abun seya saka ajikin cikinta itadai sede tai murmushi takalleshi kawai. Kaya fall suka siya. Wani gurin hutawa yabiya da ita tasha kayan sanyi. Tayi enjoying futar sosai, ranar ko girkin dare bataiba da gajiya dakansa yamata wanka yasa mata rigar baccinta me fad'i dan yanzu sutafi sawa dan tafi sakewa cikinsu. Komi yahad'ashi inda yadace kaman zasi tafiya.

~~~~~~~~~~~~~
Akwana atashi lokaci yaita tafiya wasu daka cikin dangi sun zazzo mata. Harsu Samiha Ya Hafiz yakasu ranar kuwa tasha surutu kaman karsu rabu. Inna taita aiko mata da rubutu da magungunar gargajiya dan ance mata tafara kumburi. Har cikinta yai wata 8 kaman yanzu zata haihu dole wasu abubuwan dakansa yake mata.
~~~~~~~~~~~~~

Tafiyar gaggawace tataso mai badan yasoba zaitafi yabatta tunda dama yakusa maidata gida danta haihu acan. Yanemi alfarma gurinsu Maman benua da Mijinta kan suna kula masa da ita badad'ewa zaiba danma dole ne tafiyar dabazaiba.

Dararranar kaman bazai bartaba tabashi farin ciki bakad'anba, jiyake kaman sukad'ai ne masoyan da suka rage adoran duniya. Seda yamata wanka shima yayi suka hau hira yanamaijin kama  kada yatafi batareda Queen intasaba. Seda ta lallasheshi sosai da kalamai masu kwantar da hankali dasa nutsuwa. Tausa yahau yimata yana lailaya bayanta har tahau bacci yai musu addua shima yakwanta.

Safiyar Alkairy!!!

Waiyo team Naja afuwa plsss. Makaranta abun se hak'uri. Allah de yak'aremu da lafiya. Nagode sosai didi tana sanku duk inda kuke.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:49 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*61-65*

Safiyar juma'ar dazasi tafiyar, dawuri yatashi, shara yafarayi yagyara gidan hadda kunna turare a burner.

Ruwan tea yad'ora yahau ferara Irish, yafara suya yana 6arar plantain. Yasoyawa kansa k'wai daban dan ita tunda tasamu ciki bakasafai take cinsaba. Yana cikin wanke kayan dasuka 6aci tashigo kitchen d'in ashagwa6ance tace  "kai Habibi kullum saikai ta kwashe ladan" da murmushi a fuskarshi yace "Yo ai kema kullum cikin samun lada kike, farantamin dakikema lada kike samu, ballantanama cikin dake jikinki Allah kad'ai yasan ladan da kike samu. Allah dai yarabaku lafiya. Yau ace ga 'ya'yana Jinina kuma Queen itace ta haifamin wana irin farinciki zanyi. Allah de yanuna mana lokacin darai da lafiya. "Ameen" tace takarasa gyaran kitchen d'in.

"Wanka yafarayi yataimaka mata itama tayi, suka shirya sunata soyayya abinsu. Har sukai Break-fast yakuma gyara gurin, duk saboda tausayinta dayakeji. Jiyake kamar kada yatafi ba ita.

Kaya kala uku tahad'a mai tafiyar kwana biyu zasiyi a k'aramar bus in makaranta zasu tafi awannan karan. Likitoci su biyar aka za6a zasuje workshop a jami'ar kano se driver dazai tuk'asu.

"Kamar bazasu rabuba k'arfe 9 yakaita gidan Maman Benua kada zaman kad'aici ya dameta. Haka sukai sallama tanata musu Addu'uan samun nasara da sauka lafiya, k'arfe 10 nasafe suka d'auki hanyar Kano.

Maman benua da Karamci, dukda ba Musulmai bane amma Kafiran Amanane, tun farkon zuwansu tafahimci hakan. Yanzuma cemata tai "tadena girki zatana aiko mata dashi, dandai cikinta ita kad'ai bazai gagaraba musammanma yadda tai nauyi komai dakyar takeyinsa. Ranar agidan tawuni se kusan La'asar takoma tareda Stepme 'yar Maman Benua da tatayata zama. Kallo takunna mata tashiga d'aki fes-fes dashi se k'amshi yake rigar Usmance a kan gadon ta d'auka ta rungumeta sosai ajikinta tana wasu maganganu dagaji nayabone. Sallah tai tahau had'a kayan duk daya bari kowanne a inda yadace tasakashi.
Falon tadawo suka cigaba da kallan dukda ita rabi kallo rabi tana gwada kiran wayar Usman datak'i shiga.

~~~~~~~~~~~~~

Tunda su Usman suka d'au hanya basu tsayaba se awani k'auye sukai sallar jumu'a, tafiya suka cigaba dayi. Usman yanata kiran Queen d'insa da 'yan gida amma yakasa samu. Tun suna hira jefi-jefi har kowa yai shiru, se karatu da suka kunna masubi nayi masu danna waya nayi. A Kaduna garin gwamna suka k'ara tsayawa basu wani dad'e ba suka cigaba da tafiya har suka shigo kano.

Tsautsayi daba a samasa rana/lokaci sunata sharara gudu daidai kwanar Waratu mai Tifa yafito dagudu shima yai kansu motar su Usman tai gefe se cikin ruwan dake kasan kwaltar, dukda duhun dagari yai mutane sun d'an taru sunata Salati da neman agaji abakin ruwan, motar kuwa tashige cikin ruwa sai gefanta kad'an ake gani.

"Motar wata Ma'aikata ce sukazo wucewa ganin mutane a tsaitsaye sun fara taruwa yasasu parking, dasaurinsu suk'a k'arasa bakin ruwan. Mutanen dake gurin sunyi iya bakin k'ok'arinsu suga sunfito dasu amma badama dole aka nemo fire service, suka ciro motar datacika lumtsum da ruwa. Ganin rubutun dake jikin motar suka tabbatar daga doguwar tafiya suke. A Ambulance aka d'au su Usman daba wanda yake motsi acilkinsu, motar kuma akajata da jan way. Cikin gari akai dasu General hospital ala kaisu A&E ba ai wani dogon bayaniba aka kar6esu danbasu taimakon gaggawa. Tunda sunji bayanin suwaye kuma daka inda suke.

"Mama Mahaifiyarsu Usman tunda yamata waya kafin su taso yasanar mata zaizo gida ayau Abinci iri-iri taimasa yaza6i duk wanda yakeso. Jin shiru-shiru har bayan Isha baizoba wayarsa kuma tanata kira shiru.

Naja'atu takira bayan sun gaisa take tambayarta Usman ko yakirata sun sauka? Takasa samunsa awaya. Naja'atu jitake kamar ta rusa ihu dan ita har batasan iya adadin kiran data maiba muryarta araunane tace, itama tinda yatafi wayarsa tak'i shiga, lallashinta Maman tayi sukai hangin wayar.

"Kiran wayar Samihane yasa takuma motsawa tanata tsokanarta jin Yayar tata tai shiru
~~~~~~~~~~~~~

bakamar yadda takewa samiha ba, tasha jinin jikinta, "Lafiya Maman biyu? Samihan tace tana k'ara rik'e wayar "Alhamdulillah kawai tace suka gaisa tabawa Innar wayan jin Muryarta k'asa-k'asa Innar tad'anji ba dad'i tace "Yayar Salim ko bakida lafiya ne? Kuka tasawa Innar tagaya mata "wayan Ya Usman taketa kira bata shiga dan suntaho kanon, batasaniba kowani abun yasamesu.

Hak'uri Innar tashiga bata ko matsalar network ne tabari zuwa jimawa tasake gwadawa zata sameshi, seda taji alamum tasamu nutsuwa Innar taitamata Addu'a sukai sallama kowannensu da irin sak'ar zucin dayake.

"Ad'aya 6angaren kuma a Asibiti duk wani abu dayakamata ai musu anyi Amma mutum biyune suka farfad'o ansamo numfashinsu daka Driver sewani Dr Hashir suma ba a hayyacinsuba. Suka cigaba da duba sauran. Ganin haka yasa suka kira Vc University aka sanarmusu.

Dolensu suka kira Guadians d'in duk wanda akai tafiyar dasu. Mahaifin Usman suna tsaka dacin abinci dare wajen k'arfe Tara nadare sak'on yariskesu. Bak'aramin tashin hankali suka samu kansu acikiba dajin labarin. Abincin da basu gama ciba kenan suka tafi General Hospital sauk'in abunma agarine.

"Ward d'in da aka kaisu Usman suka nufa. Usman gashinan akwance kamar ai magana yatashi yai wani fayau dashi. Kukan da Mama tasane Alh yarik'ota bashiri sukai waje alokacin yasanarwa da 'yan gidansu Naja'atu. Adaren wasu sukazo har Inna k'annan Usman ba abin suke se kuka manyan nata Lallashinsu. Anan kuma tunanin kowa yakoma kam Naja'atu baiwar Allah idan taji yazatayi ga tsohon ciki. "Hasbunallahu wa ni'imal wakeel" shine abinda sukaji Inna tahau fad'a.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:49 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*66-70*

""Nannauyan numfashi Abban su Usman ya sauke, wajen 12na dare suka bar Asibitin. Baban su Naja'atu da Abbansu Usman sun tattauna sosai da Likitocin inda suka sanar musu da tashin Usman se wani ikon Allah.

Washegarin ranar tun bayan asuba Abban suka koma Asibitin ko Maman bai yarda taje alokacinba sha'anin mata saisu. Tin kafin Likitan yagamai masa bayani ganin Usma d'in a lullu6e yatabbatar da zarginsa yazama gaskiya, wasu zafafan hawaye yaji suna bin fuskarsa, "Allah sarki Usman Ubangiji yaimaka Rahmarsa yaro mai biyayya da girmama nasama dashi. Allah yasa Mutuwa tazama Rigar hutu agareka." Addu'a sosai yai masa yashare hawayen dasuka zubomai. Duk wani ciki-cike yayi dan abashi gawar Usman d'in gida. Tun a Asibitin yaja gefe yana buga waya duk wanda yakamata yasani.

Kiran V.C in Jami'ar da suka aiko su Usman d'in Worlkshop wanda akan hanyarsu suka

sami Accident. Tun awayar yafara masa Ta'aziya dan tun cikin daren sak'on mutuwar wasu daga cikin D'alibansu kuma Likitoci ya riskesu. Anan Abban yanemesu su sako Matar Usman ajirgi akata Kanon sabida cikin dake jikinta, zatai kumburi intai zaman mota tunda tafiyace ba kad'an ba. Yace "bakomai za ai hakan dayardar Allah" suka aje wayan. Kafin 8 nasafe sunda gida Mutane har sun fara zuwa dole aka maida Jana'izar 11 nasafe. Musamman sabida Naja'atu itama tai masa addu'a dafatan samun dacewa da tafiyar. Mama kuwa saida Abban yad'aureta da jijiyoyin jikinta kada tai kururuwa. Duk da haka suma tai da aka shigo da gawar Usman d'in.

"Naja'atu kuwa V.C in suna gama waya da Abban Usman tingari baigama haskeba suka nufi Staff Quaters in, tareda matarsa Yarabawane amma Musulmai ne, matar tabashi shawaran su nemi taimakon Naibours insu. Baban Benua shiya bud'e k'ofan ganin V.C dakansa yasashi rusunawa suka gaisa cikin yaren Yoroba bayani sukad'an masa yataso Maman Benua si musu taimako seda tafito yadda bazasi musu kwarwa ba V.C yasanar musu Dr Usman Mak'ocinsu dawasu likitoci da aka turasu Workshop sun sami Accident, har wasu sun rasa rayukansu. V.C yace "Gidan Usman d'in zasu rakasu" Maman Benua kuwa k'ara tasa tareda d'ora hannu akai tafara "Oh my Goodnees woo!" Dak'yar matar V.C tabata baki tai shiru. "Matar za a tura injishi, ance ciki gareta suje ahad'a mata kayanta duka za aturata kanon a Jirgi.
Naja'atu tana daka kwance tunda tai sallah takasa rintsawa tunane-tunane kawai take da sak'ar zuci, wayarta kuwa har tamutu sabida neman wayan Usman batareda tasameshi ba. Jin bugu yasata tashi dak'yar seda tatsaya taja numfashi had'e da zumbula Hijabi kan faffad'ar rigar baccinta har k'asa, tanufi k'ofar.

"Bak'armin tausayamata sukaiba ganin idanunta duk sun zuge, tunaninsu tasan abinda yafaru "Am so sory" shine abinda sukee cemata, itadai basu guri tai suka shige ganin harda Mak'otanfa. V.C yai mata bayanin abinda yakasu batai musu musuba, suka shiga tattara mata kayayyakinta. Maman Benua da Lokaci-lokaci take share hawaye a wayance karta k'ara birkita Naja'atun, suka tattaramata duk kayansu itada matar V.C. dukda haka seda Maman Benua tahad'a mata kakkauran shayi wanda dak'yar Naja'atun ta iya sha. Sukai musu sallama.

"Dawani captain Oba V.C yahad"ata dan basu samu jirgin dazaije Kano awannan safiyarba se Abuja inda acan sukesa ran samun mezuwa Kano kafindai Ranar ta bud'e. Akasai mata ticket Kayanta duk aka shi cikin jirgin. K'arfe takwas nasafe sukai Abuja.
A canma bayan 'yar hada-hadar dasukai Allah yataimaka dakwai jirgi mai zuwa Kano daga abuja ticket aka kuma siya mata kafin 11nasafen sun isa Kano. Babansu dakansa yazo d'aukarta shida yayunta biyu da Samiha. Dalabinta take k'ok'arin tsugunawa tagaidasu Baban yai saurin dakatar da ita. Idanun Samiha taga sunyi ja sosai, bade wanda yace mata komai sukasa duk akwatunanta amotar suka tafi Baban nasu yana k'ara tausaya mata. Ganin k'atotan cikin dake jikinta duk abinda keciki yazama *Maraya* yanzu kuma taje tatarar da Mummunan labari. Da dabara yashare hawayen daya zubo mai batareda wani yaganiba.

Naja'atu kuwa ganin sunyi hanyar sharad'an tunaninta ko gida zaikaita, zuciyarta tai wani bugu ganin ciccirindon mutane tun daka farkon layin, har suka zo gidan Mama. Jitai duk wani k'wari datake dashi ya salu6e motsi ma dak'yar takeyi kanta tahau tambayar meke faruwa anan?

Dukda haka takuma kumburi akan nada
Kasa fitowa tai daka motar dole Samiha da Baban suka fito da ita takunma dak'yar take, tunanin Mijinta yahauyi da  Usman ne seya had'ata da jikinsa, ya tallafota yanayi yana mata sannu cikeda kulawa suje duk inda zasu. Toko ina yake daba'azo d'aukarta dashiba? Cikin gidan suka nufa, nanma ganitai mutane dayawa dangin su Usman Mata da Maza yawanci duk sun zubo mata idanu. Ahankali tafurta Mamace tarasu? Jikintane yahau rawa. Baban su kuwa tak'ofar gaba suka shigar da ita falon Abbansu Usman da mutane da dama a falon wasu daga ciki sunci kuka Yusra yayar Usman tana ganinta takuma sa kuka. Jitai wasu nafad'in "Mutuwa mai yankan k'auna kinga matarsa da tsohon ciki, jitai cikinnata yawani hautsuna har tana naman durk'ushewa.

"Agaban gawar Usman d'in aka ajeta. Kwance yake amik'e anmasa sutura nannad'e da Likafani ankuma yafa zani akai. Idanuwanta takai kan mutanen falon kowa taga yananan har Innarsu cikin jimami da taraddadi y
Suke, to bataga Mijinnataba. Hannu takai tana shafar jikin zanin da aka lullu6e gawar Usman dashi
 "Kiyi Hak'uri Naja'atu *Kullu nafsin za'iqatul maut/ kowane rai seya d'and'ana zafin mutuwa*.kowana lokaci takan iya riskarmu to Allah daya fimu sanshi yakar6i abunsa.
"USMAN NE NE KO BABA? Abinda ta iya fad'i kenan dayawa agurin sunji tausayinta. Dan bakasafai zakaji ta ambaci *Usman* d'inba. Gaba d'aya iyayen suka matso kusa da ita suna banbaki da nasiha "tayi hak'uri da tawalkali wataran kowa in lokacinsa yayi seya amsa kiran Ubangijinsa. Karki tumami dan
*Annabi S.A.W yace "Basa tare damu, #Masu marin fuskokinsu, #Da masu yaga Aljihunansu, #Da masu D'aga murya suna kira irin Na Jahiliyya. Ayayinda akai Mutuwa. @bukhari da muslim ne suka rawaito.*

"Kiyi masa addu'a zaitafi gidansa nagaskiya muma wataren mune haka" Inji Maman Usman tana dafo bayan Najar.
 "Allah yai masa rahama yakyautata namu zuwan" abinda ta iya furtawa kenan. Dukkansu sunaji suna gani musamman Naja'atu da jinta take kamar kara cikimma tanemeshi tarasa haka aka fita da Usman d'in akai mai Sallah suk tafi kaishi zuwa kushewa.

Semuce Allah yajik'an Muslim Umma. Ameen.!!

@Team naja'atu kuzo mujewa Naja ta'aziyya gsky
#sharar hawaye!!!

© *Didi_sady*🍼🍉😜
[2/18, 10:49 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*

*Haleema G Khaleel*

*71-75*

""Tunda aka fita dashi ta d'ora idanuwanta kan k'ofar, gani take kamar a mafarki. Lallai Rayuwa batada tabbas, yanzu kake Mutum yanzu zaka iya zama Gawa. Shiyasa ake so kazamto mai aikata Alkairi arayuwa kazauna da mutane lafiya yadda kobayan ranka Kyakykyawar Shaida zata rik'a binka. *Hak'ik'a duk Mutumin daya manta Allah to tabbas yana tareda Shaid'an*. Allah Yai mana muwafak'a. Ameen.

Haka tazama kamar Mutum Mutumi, tana kafe aguri d'aya kamar gunki. Motsi ma kasawa tayi bare Kukan dataga dayawan mutan gurin nayi, wani irin d'imuwa tasamu kanta aciki, bugun da zuciyarta tayi hasseda taji Motsin abunda ke cikinta, kuka takeso tayi kota samu raguwar Nauyin da K'irjinta.

Cikin kwanakin Naja'atu tazama komai sede aimata ko magana bayinta tacikaba. Abinci se anyi kamar anayi zataci shima kad'an. Tabi tarafke tayi wani bak'i se k'atotan ciki dake jikinta. Damuwace sosai tattare da ita. Agidan su Usman d'in take kwana.

D'akin Maman suke kwana itada k'anwar Maman Yaya Yusra da 'ya'yanta se autar Maman. Bacci ma sede 6arawo ya d'auketa duk tabi tad'ashe tazama wata iri da ita.

Daren ranar da Usman yai kwana uku darasuwa, Naja tana kwance dare yatsala tunanin rayuwar ta take harta gangaro kan zamantakewarsu da Usman cikin Aminci, Yarda, K'auna, Kulawa da Soyayyar junansu. Lokaci d'aya Allah yad'aukeshi daga cikinsu badan baya sanshiba, tatuno yadda yake san cikin jikinta tunkafin tahaifo shi irin burin daya d'ora akan abin dayake cikinnata. Kuka tasaka mai tsuma zuciyar mai sauraro, tin tanayi a 6oye har shashshek'arta tafito fili, Yaya Yusra dabata jima da komawa bacci ba, taji alamun kukanta tashitai tareda kunna fitilar wayarta tahaska kan gadon , jijjigar dataga jikin Naja'atun nayine yatabbatar mata da ita keyin kukan, gadon tanufa itama kamar jira take tasa nata kukan har Mama tashigo d'akin ganin suna kuka zuciyarta tak'ara tsinkewa, bata hanasu kukanba musamman Naja'atu dasukeso tayi kota samu ragin damuwar datake ciki.

Batasan sanda itama hawaye yakecemata ba har wani nabin wani. Maman tai dauriya tai shiru Yaya Yusran ma, ita kuwa Naja'atu seda tai mai isarta Mama tatasheta tareda jingina ta ajikin pillow Ruwa tabata tasha sannan suka hau lallashi da nasiha tareda bata Misalai iri-iri na Rayuwa itadai jinsu kawai take.

Cikin kwana bakwai darasuwar, sunsha bak'i daga 6angare daban-daban dayawa kuma sun mata ta'aziyya. Har 'yan gidansu dukda irin zaman doya da manjan dasuke. Zuwa lokacin ta kuma rama ba kad'an ba. Zagayayyar fuskarta tayi fayau da ita. Danna Inna kullum saitayi mata tofi cikin zam-zam tanasha, Addu'oi dadama take mata banda wanda tabata takeyi. Taga kuwa fa'idar hakan dan damuwar datake ciki taragu sosai. Tafauwalawa Ubangiji duk lamuran rayuwarta shiyasan miyake nufi dayai mata haka.

Bata kuma rikicewa ba seda aka kawo kayan Usman ranar dayacika kwana takwas darasuwa,

taga abubuwansa dayawa komai yananan shid'in ne babu yatafi inda ba'a dawowa. Aranarma tasha kuka wanda har zazza6i yasaukar mata.

Kwananta goma gidansu Usman d'in. Alh Abdul-Mu'iz mahaifin su Naja'atu dakansa yanemi takoma gida dukda anriga anzama d'aya nanma gidane. Ganin irin damuwar dake tattare da ita, bayan hakama komai sai anmata. Hakan yasa sukace "zasu tafi da ita gida. Mama kuwa sotai abarta agurinsu har ta haihu. Kayanta duka aka kaimata gida tasha kuka harsu 'yan gidanma haka tatafi tana ganin kamar rabuwa sukai. Itada zuwa kuma se ikon Rabba. Danma zuriyar data shiga tsakaninsu in Allah yaraya abinda zata haifa.

Har sukaje gida bata k'ara cewa k'alaba, dasukaje gidan nema bayan anfito da ita daga motar wasu daga cikin 'yan Mazan gidan dasuka tarar a harabar gidan suka k'ara yimata ta'aziyya. Da hawaye tashiga gida. D'akin Innar aka gyara mata bayan gadon dake d'akin, k'atuwar katifa baban yasaimata aka samata daka gefe daduk sauran kayanta aka shirya mata, kwanciya tai tanata maida numfashi. Tafad'a duniyar tunani har bacci yai awon gaba da ita.

Zamanta agidan tun bayan dawowarta bayabo ba fallasa. Duk abinda takeso dai-dai gwargwado tanasamu. Matan gidan sunanan da halinsu, danma bakasafai take fita ba daga zuwa Asibiti dashima tafi zuwa dadare, se d'an atisayen datake zagaya cikin gidan. Ahaka har cikinta yashiga wata tara. Haihuwa yau ko gobe. Inna duk tatanadi kayan jego da ake buk'ata gamai haihuwa tashirya. Hatta kayan mai jegon duk tashirya sejiran Allah yasauketa lafiya. Zuwa lokacin Usman yayi kwana  Arba'in harda d'oriya da rasuwa.

Sosai take kewarsa, danma Inna tayi namijin k'ok'ari wajen hanata zuzzurfar tunani. Data fara zatai tabata hak'uri da nasiha harta samu tasaki jikinta. Maman Usman ma tana yawon zuwa dubata banda aiken datake mata. Haka itama Yaya Yusra tana tafe da abubuwan arzik'i duk dan ragewa Naja'atun damuwa da kewar babban rashin datayi.

Afuwa makaranta ankusa k'arka'arewa da yardar Allah.

© *Didi_Sady*🍼🍉😜

[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡

*Na*

*Haleema G Khaleel*

*76-80*

""Tun suna saran haihuwarta har EDD haihuwar yazo yawuce, ba abinda kedaminta se kumburin dajikinta yake gawani haske da d'ashewa daduk jikinta yayi.

Wata safiya suka nufi Asibiti da ita dan tun cikin dare take abu guda, dak'yar ta iya Sallah asuba. Dan itama Sallar azaune take tunda cikinta yatsufa. Abincin da Inna takawo mata taga bata bud'a komaiba. Tana kishingid'e sefitar da numfashi take da k'yar duk tahad'a gumi. Inna ta tallafota tareda jinginata ajikin garun d'akin "Inna Bayana ciwo" Naja tafad'a dak'yar.

"Subhanallah! Badai abinne yazoba? Ina zuwa" Innar tafad'a tafita daka d'akin.

D'akin Mama Luba Uwargida tashiga tasanar mata "ko zatazo takai Naja'atun Asibiti tunda itace babba agidan. Bud'ar bakin Mama Luba secatai "Ita gaskiya bazata iya futaba dan bak'i zatai, yanzuma zaman jiransu take suna hanya." Inna mai sauk'in kai takuma cewa "dama dan kada abin yazama laifi shiyasa tazo tagaya mata dan abata girmanta na babba agidan... bata idasa rufe bakiba Mama Luba tace "kinga dan Allah banasan hayaniya kinzo kin gayamin tunda nace bazaniba a hak'ura mana". Sum-sum Innar tafita tana Addu'ar Allah yanuna mata ranarda mutan gidan zasu shirya.

To yadda sukai da Mama Luba haka sukai da d'aya matar gidan wato Goggo Safiya ita cewa tai ma "Unguwa zataje taje takaita mana su innasune wasuke nema yakai musu. Ranar Inna ranta ya6aci sosai, dandai kawai batada dangi agarin za'ana yimata haka. Samiha tanemo a waya, suka rufewasu Fawad d'akin insun dawo tunda kowa zai iyaima kansa komai dama Deedat takeji inyada yaga batanan.

A Napep suka tafi Asibitin ko Alh bata sanarwaba. To duk zaman awannin dasukai Naja'atu bata haihuba aranar. K'arshema dawowa gida sukai wajen Maghriba da aka tabbatar musu da cewa "ba haihuwar ceba. Haka Naja taita fama saida taikwana biyar ahaka.

Zuwan da Maman Usman tayine suka yanke amaidata Asibiti.kar aje asamu matsala da abincikin ko ita uwar. Da wannan shawarar sukai amfani. Motar da Maman tazo da ita suka kaira Asibitin. Basu nemi kowaba dan ita kanta Maman d'an zuwan datake gidan tafahimci irin zaman dasuke agidan. Dandai su Naja'atun da Mahaifiyarsu sun maida komai ba komaiba sam abin baya damunsu dan dole wataran zasu dena ko duniya tabasu darasi. Lallai hausawa sunyi gaskiya dasukace *"DUTSEN CIKIN RUWA..BAISAN ANA RANA BA"*. Asibitin Nagari Hospital & meternity sukaje dan tun dawowarta Kano nan take zuwa.

Tun rana da aka kaita Asibitin Naja'atu take abu guda Nak'uda sosai take likitan dake Dutyn Ranar yana kanta har dare lokacin tashinsa yai. Zuwa daren duk k'arfinta yabi yak'are Mama sai mulmula mata bayanta take. Dr nafeesa datake dutyn daren tana zuwa lavour room d'in taga yadda Naja'atun tayi cikin yabi yarairaye yai k'asa iya galabaita tayi bata haihuba. Kayan aiki aka had'a mata da taimakon wash Nurses suka shirya Naja'atun Dr Nafeesan dakanta taturata zuwa ```Theater room``` Emergency C.S zatai mata takadda tabasu sukai singning akai ciki da ita.

Inna Addu'a take ta mata. Suna zaune jugun-jugun. Jiran tsammani har goma da rabi na dare. Dr Nafeesa kuwa suna kan Naja'atu itada Dr Moses da sauran nurses. Baby boy akafara cirowa sannan aka ciro 'yan mata guda biyu d'ayardai andenneta sosai acikin. Yara kamar mahaifinsu duk aka gyaresu sede wadda aka ciro ta k'arshen ita sam batai kuka ba. Dr nafeesa da Dr Moses suka rik'o 'ya'yan tareda wata Nurses suka kawasu Inna yaran. Se farinciki Mama cema tai k'arfin halin cewa Ina Maman tasu bata gama maganarba aka turota akan gado zuwa d'akin hutu aka shigaddasu duka da ragowar kayanta.

Yaran annad'esu a showel harsu uku, Maman Usman kuka tasa sosai da ganin yaran, yau ga jinin Usman alokacin da Usman yabar duniya. Batareda hayaniya ba sukaita d'aukan yaran

sud'au wannan su ajiya sud'au wancan. Maman Usman kuwa ga hawaye ga dariya duk afuskarta. Waya tasa tana tai musu Hotuna jitake kamar tamaidasu ciki sekace yanzu akafara haifa mata Jikoki. Inna har tausayinta taji.

Se wajajen shabiyu suka bar asibitin akabar Inna da Samiha. Cikin daren yaran sekuka suke mace d'aya da namijin, d'ayar ko motsawa batai ba. Zam-zam Inna tasa dabino aciki taita basu suna sha, se jijjigasu suke seda sukai bacci suma suka runtsa dukansu.

Da Asbah bayan sun idar da Sallah Dr Nafeesa tashigo dubasu dan dawuri zata wuce. Anan Inna taimata complaining kan d'ayar babyn sam batai Kukaba ko motsi bataiba. D'agata Dr tayi tak'ara jijjigata amma shiru overall d'in Jikinta tayaye duka tad'an d'ala mata, nanma shiru, tak'ara jijjigata ba alamun numfashi tace "I think so dama itace ak'arshe kuma biyun sundanneta dakuma galabaitar da mahaifiyarsu tayi yataka muhimmiyar rawa. Batazo da rai ba." Atafi da ita gida abunne. Allah yaraya sauran yabada masu albarka. "Haihuwar farine ko? Dr Nafi tafad'a tana kallan Inna tareda mik'a mata Jaririyar. Tai musu sallama tatafi idan incharge na safe sunzo zasu duba Naja'atun may b kafunnan ta farfad'o.

Karfe 7 nasafe Maman Usman tazo hae har Yaya Yusra, lokacin sukaita bugawa dangi nakusa dana nesa waya. Suna sanar musu da haihuwar. Mik'o mata Matacciyar Jaririyar Inna tayi tace "wannan bata da rai kutafi da ita gida a bunneta". Allah sarki Mama tace "Allaj yai bame shan wuyar duniya bace." Can Sharad'an suka tafi da ita aka binneta inda aka kai mahaifinsu.

Lokacin dasuka dawo har Alh dasu Sadiq a sannan Naja'atu ta farfad'o. Likitan daya karb'i dutyn safen shiyazo dubata yace "kar abari tai jijjinan motsi sosai, espcly kafarta sannan subata ruwa ko abinci mai ruwa-ruwa, banda abu mai k'ayau. Yafaffad'a musu duk irin abubuwan daza ai mata dawanda bazataiba.

Dataimakon wata Nurse tai brush, aka bata shayi sannan suka gyarata. 'Ya'yan data haifa aka ajiye mata kusada ita sunsha wanka sai k'amshin turaren jarirai suke. Tana daka kwance 'ya'yan duk agabanta, kallansu taitayi cike da k'auna, wata soyayyar yaran taji tanabin kafofi da jinin jikinta. "Kamarsu d'aya dashi ko Yaya Yusra? Naja tace da Muryatta dabata gama warwarewaba, k'wallace tabiyo bayan maganar tata, itama Yaya Yusran sun bata tausayi sosai taji itama kamar tasa kukan, dandai kadata k'ara bata k'arfin gwiwar yin kukan yasata danne zuciyarta. Anan suka sanarmata uku tahaifa sedai d'ayar batazo da raiba. Zaro idanu tayi tace "duk acikina, lallai Iyayenmu sunsha d'awainiya damu. Kuma dole miyi Biyayya agaresu tahanyar dabata sa6awa mahalicci ba muddin munaso mu wanye lafiya a duniya. Alllah yasaka musu da d'umbin Alkairu yabiyasu da babban rabo. Allah yak'ara bamu ikon cigaba da faranta musu dayi musu biyayya bisa turbar Islama. Itakuma Allah yamata rahma yakyautata namu k'arshen. Duk mutan d'akin suka amsa da Ameen.

Kwanansu biyar a Asibitin mai jego tawarware sosai, har tana shayarda yaran. Namijin mai hak'uri, macen kuwa rikici gareta. Danna Inna da Samiha basu gajiya da d'awainiya dasu ko kuka suke tana bacci ba kasafai suka fiya tashintaba. Inna takance "batta tai bacci tad'an samu hutu, ita kada'i tasan gumurzun datasha daga rainnan ciki har haihuwarsu." Dukda dai kowace mace da kalan nata abubuwan.

© *Didi_Sady*🍼🍉😜
[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN  RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*81-85*

_Afuwa Makaranta wannan labari. Bajan rai bane kunsan d'an adam ajizi ne. Abubua sunyi yawa. Kwana biyu kuma banida Ipy. Ga bukukuwa da aketayi a fam. In sha Allah before Jan 2017, zan kammala. Nagode da k'aunarku gareni aduk inda kuke._

~~~Aran kwana bakwai da haihuwar aka sallamesu da rana. Duk wani kud'i da aka kashe tun farkon zuwansu Asibitin Baban Usman ne yabiya, dan cewa yai "Haryanzu da nauyinta akansu, dan haka duk abinda ake buk'ata yace "Agayamasa" Mama kuwa suka 6alle bakin aljihu akai komai cikin mutunci da girmamawa.

Bare dasukaga anhaifar musu Tagwaye. Kayan barka sosai suka siya ranar dasuka koma aka bisu da tukwici dak'yar suka kar6a. Acewarsu "Ai yiwa kaine anriga anzama d'aya.

Ranar suna kuwa bawani taro akai ba. Rad'in suna akai aka sawa Namijin sunan Usman itakuma macen aka samata Asma'ul Husna. Samiha tasa musu Hassan da Husna. 'Yan barka sukai tazuwa 'yan uwa da abokan arzik'i. Kayan barka iri-iri suka samu, wasuma sa shekara suna amfani dashi.

Mejego tayi k'alau da ita. Dan jego mai kyau ake mata har sukai wata biyu. Yaran sunyi 6ul-6ul dasu, kamarsu da mahaifinsu se dad'a baiyana take. Ita kanta Naja'atun kamar ba ita ta haifesu ba, dan gyara sosai Inna da taimakon k'anwarta Aunty Husna sukai mata. Irin zugudan nan dayawan masu ciki keyi bayan haihuwa, basu bari tayiba.

Tayi k'alau da ita. Sedai idan takalli yaran nata takanji tausayinsu natashi dazasi basuda mahaifi. Tak'udurce aranta bazata ta6a bari siyi Maraiciba.

Duk yadda zatai takare Mutuncinsu zatai wanda bai kaucewa shari'a ba. Kuma ga kakannunsu da dangin mahaifinsu dasuke sansu da ji da k'aunarsu.

*BAYAN SHEKARA HUD'U*

Hangota nai cikin _Nagarta Shoping Complex_ d'auke da basket a hannunta. Deedat nagani yak'ara  girma rik'e da hannun wasu yara masu kyau dabazasufi shekara uku da rabi ba. Mace da Namiji, kalan kayansu iri d'aya, sedai Bambanci na Mace da Namiji. Macen anmata kalba datasha Bead se reto suke ajikinta.

Tsayawa tai wurin kayan k'amshin gida tanata duba irin wanda takeso. Domin ita
~~~

ma'abociyar k'amshi tundaka najiki zuwa na d'aki hakama kyawawan 'yan biyun 'ya'yanta Hassan sa Husna.

Naja'atu kenan matashiyar Bazawara, datun bayan rasuwar Mijinta bata sakeyin wani auren ba. Asalima catai ita tagama, seda mahaifanta suka tsaya tsayin daka da Addu'a da rok'on Allah tasaki ranta tadawo da walwalarta daduk wata mu'amala harta koma Makaranta da D.E daga level2 tafara har take shekarar k'arshe a course in ```Nursing and Nursing science```.

Jitake zata iya Aure ayanzu, kowaye yazo muddin yanada d'abi'a da mu'amala ta k'warai, kuma yakwanta mata tayi Na'am dashi da wanna tasamu tarufe bakin Iyayen nata. Ganin ana shirye-shiryen Auren Samiha da sauran k'annanta Mata, amma ita shiru.

K'wace hannunsa Hassan yayi, daga hannun Deedat ganin Husna tayi gurin toys dandama tafishi wayo. Da gudunta nayara tayi gurin toys tagano 'yar tsana, Bangazar mutumin dataine yasata tsayawa. (Sanadi😻)

Agogon daya d'aukane samfurin ```Dior``` yafad'i daka hannunsa har saida Glass in ya tsage. "Ya salam! Ya furta da _Husky voice_ insa mai amo. Irin yawan dayasha yana neman ```Wrist watch``` in besamuba se anan gashi yanzu kuma abinda yafaru ko biyan kud'inshi baiyiba, cikin jin haushi da takaici afuskarsa yad'ago zai mata masifar wata irin matace dabata tafiya a hankali? Tajamai wannan d'anyen aikin. Batasan irin wuyar dayasha yana abu guda naneman brand na Agogonba.

'Yar k'aramar yarinya kyakyawa idanuwansa sukai tozali dasu.
Husna kam ganin yasha mur bashiri takama kunnuwanta tai kalar tausayi tace "Am sory Uncle" ai saurayin besan sanda ya murmusaba yaji yarinyar ta burgeshi sosai. Inama 'yar sace, tunano yadda Mahaifiyarsa babu abinda takeso irin yayi Aure, har matakaiga samun zuri'a.

Shafa kanta yai yace mata "Be careful kinji Babyta next time kirik'a tafiya a nutse karkije kima wani irin tawa yadakeki, bama haka ba kada kiji ciwo kinji." D'aga kanta tayi alamun taji tace "Thank you Uncle" Matashin saurayin yace "Oya give me five" yabata hannunsa suka tafa sunata dariya.

Hassan ganin ba a daki Husna ba, sunata dariya, shima yataho yana dariya dabaisan akan me ake ba.

Da mamaki afuskarsa yake kallansu duka. Mik'amai hannu Hassan yayi da nufin su gaisa. Saurayin kuwa yakama d'an hannun Hassan suka gaisa. Tsugunawa yai dai-dai tsayinsu yace "U are identical 2wins?" Saboda tsananin kamanninsu yayi yawa. Yakuma fad'in "Am i right?" Yana cigaba da kallansu.

Husna da surutu takuwa hau zuboshi "Mamynmu tace mu Triplet ne amma d'ayar tamutu ita bamugantaba.

Dariya yahauyi sosai daya jima baiyi irin taba. Yace "Shikenan nikam nayi new friends yau, amma bansan sunankuba."

Husna takuma cafe maganar tace "Mu 2wins in Mamynmune yanzu amma sunannu ni tanuna kanta sunana Husna Usman Bello Galadima, shukuma Hassan sunanshi Usman Usmab

Bello Galadima, sunan Babanmu aka samai shine ake cemasa Hassan. Amma har yanzu Abban bai dawoba Mamy tace "Yayi tafiya inda ba a dawowa. Shiyasa bayanan.

Kuma mu kullum baya d'aukomu a school, sukuwa su Farouk Abbansune yake zuwa d'aukansu." Tafad'a tareda kama hannun Hassan. Shima yace "Se Mamynmu ko Uncle."
Sunbashi tausayi sosai, yafahimci komai wato Mahaifinsu yarasu basuda wayo ko ba a haifesuba.

Kama hannayensu yai duka yace "Tare dawa kukazo gurin nan?
Hassan yace "Da Mamy da Ya Deedat. Batasan munzo nanba dan tace mudena surutu inba Alkairi mutum zai fad'a ba yai shiru. Har Rok'o dayawoma tace. Ana sace mutum inyaje yawo inda baisaniba yadena ganin kowa har Mamanshi." Ko Husn Yafad'a yana kallan Husna. Surutun kuwa sukai tamasa yanata record dan sun birgeshi. hadda tambayarsu to in aka saceku yazakuyi. Zaro ido sukai suduka. Husna datafi wayo tace "semu kira Mamynmu awaya ko Uncle Isma'il da Ibrahim."
Yace "To tayaya zaku kira?" Digit tahau fad'omasa yanata mamaki.

Jiyai sunkuma shiga ransa, kamar yatafi dasu tunda duk yaji details insu har Adress in gidansu dana kakanninsu. Suka gayamai yaran masu d'ankaren surutu kamar sunci Kabarai. Ga wayo. Kuma ai shima 'ya'yansane. Tunda hausawa sunce *D'a nakowane*
Tinanin dayai idan yatafi dasu Mahaifiyarsu yazatai dan ko ina take bazataji dad'i ba. Toma haka ake daka ganin Sarkin Fawa sai Miya tai zak'i Koshi bazaiso amai haka ba. Dankuwa sai inda k'arfinsa yak'are.

Yace musu "Shi sunansa Uncle mai zane, daga yanzu yazama Uncle insu shima. Sukuma sun zama Friend d'insa. Suka tafa dukansu. Sunata mumma, yama manta da batun Agogonsa.
Zagaye sukai tayi, yasai musu toys da chocolate, wafer,biscuit dayawa. Aikam yasha godiya gurinsu.

Sukaje aka biya kud'in. Har waje yarakosu, kaya taganosu dasu nik'i-nik'i. Ita Husna ma jan kayan take.
Nemansu take tayi har suka futo zasu shiga mota. Cogewa tai tana kallansu se muzurai suke.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: *♡DUTSEN CIKIN RUWA.....♡*
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*86-90*

~~~Yaran sunsan in Mamyn tasu tai shiru, tana kallansu sunyi laifi kenan.
Tun basu fahimtaba, har suka gane me shirunta kenufi, dukansu suka saki kayan hannunsu suka kama kunnuwa atare sukace "Afuwa Mamy" ganin tayi shiru batace komaiba suka k'ara langa6ar dakai, kalar tausayi sukai sosai.

Shigewa mota tai kamar zatatafi basu, da gudunsu suka taho har Hassan yakusa kifewa, "kayanfa wakuka barwa" Mamyn tasu tace, tana kuma kallansu, tasha mur. Suma d'if sukayi suka sunkuyar dakai.
Bud'e motar tai atsawace tace "Kushige mutafi, zakusan kunje yawo daga zuwa daku harda rok'o, punishment zaku kwana kunayi, Abincima bazakucuba tunda bakujin magana.

Ai bata k'arasa maganganunta ba suka shige motar dasauri suna kuka dukansu jin hukuncin daza amusu.
Duk abinda yafaru yanadaka gurin k'ofar shiga _Complex_ in yana hangosu,"dukda baiga fuskartaba, hakan datai musu yanuna tanasan sukasance cikin tarbiya, ba kwad'ayi dasan abin duniya ba.

Kayan dayasimusu suka bari, yazo yad'ibesu amotarshi yasa, yabar gurin shima ko siyayyar dayazoyi baiyiba. Direct gida yawuce.
Mahaifiyarsu dasuke kira da Umma, tana zaune littafin *Garkuwar Musulmi* ne a hannunta tana dubawa, da Sallama yashiga falon. Ganinshi tai d'auke da kaya. "Sannu da gida Umma" yace tareda zama. Ummantasa tadubeshi da kulawa tace "Harka dawo ashema ba jimawa zakaiba, afitarba?"
Ajiyar zuciya yasauke yace "Ah Umma d'an akasi akasamu a inda naje.
Anan yakwashe komai yagayamata, dan itace abokiyar shawararsa tun yana k'arami, shi ko yawan abokanai bashida su. Ummansa itace kominsa, har _recording_in surutun di Hassan da Husna yakunna mata taji, na dariya tayi na tausayi ta jimanta, yad'ora dacewa "Shifa gaskiya seya bisu yakai musu kayan" yashige d'akinsa. Umman tasu tabishi da kallo aranta tana Addu'ar Allah yabashi mata tagari dazata kuladashi. Shima yai Auren koya dad'a samun nutsuwa arayuwarsa.

Arc Sulaiman Tajuddin Kazaure shine sunansa. Mahaifinsa Alh Tajuddin Hafiz Kaxaure da mahaifiyarsu Hajiya Maryama. Asalinsu 'yan jihar Jigawane, Aurensu tunna Saurayi da Budurwa, Allah ya albarkacesu da 'ya'ya Hudu duk Maza, Muhammad Kabir shine Babba Barister ne mai zaman kansa, suna zaune a Abuja tareda Matarsa Farha da 'yayansu uku.
K'aninsa Tasi'u shima da iyalansa su suna zaune a Kazauren inda yake aiki. Mebimsa Yusuf dabai dad'e da Aureba yatafi da Amaryarsa can Bony a Phorthacoat inda yasamu Aiki.

K'araminsu shine Sulaiman matashi dabai haura shekara 30 ba, Archtecturing yakaranta a Jami'ar ```Kano University of Science and Technology dake Wudil ```A Kano . Zane zane da Allah yabashi baiwa da fasaha akan haka, Taswirar Gidaje da Ma'aikatu har mutane ma,
~~~

yamaida kai sosai akan harkar tasa. Allah kuwa yasamai Nasibi acikinta. Hayarsa ake d'auka gari-gari wani sa'in har wasu K'asashe . K'ark'ashin kamfaninsu mai suna _"The Shariff Construction"_.

Suna zaune a D'an Agundi G.R.A, dake Zoo road, sakamakon Aiki dayada da Mahaifinsu Ma'aikatar Ruwa ta Hadeja-Jam'are, reshen jihar Kano.

Hajiya Maryama mace ce mai tsafta, kawaici dasanin yakamata, uwa uba rik'o da Addini. Ga zumincin 'yan uwa nakusa dana nesa, duk ta d'ora 'ya'yanta akan
turbar hakan.

Allah baibata haihuwa dayawaba, shiyasa takeso Sulaimanu in yai Aure yazauma kusa da ita. Kota rik'a ganin 'yan kufi-kufi akusada ita. Duk sauran 'ya'yannata da iyalansu sunmata nisa.

Wannan kenan.

Naja'atu dasuka koma gida ko kayan data siyo bata idasa ajewaba, takamo 'yan biyun nata Hassan da Husna "Kneel down & close your eyes" tace tana zare idanu. Bashiri sukayi atsorace bawanda yace uffan.

Harta gama jera kayayyakin, ta adana komai inda yadace. Abinci tazubo dantaci, kasa cin abincin tai, dan tasaba yanzu tare dasu takecin Abincin. Abunka da Uwa da d'a tausayinsu yatasomata, janyosu tai duka tarungumesu  tsam ajikinta kamar za'a k'wace matasu.

Hak'uri suka bawa Mamyn tasu, taja musu warning sosai, suka fara cin Abincinsu cikeda ladabi dan duk takoyar dasu Ladubban ci dasha:-
*Kaci da hannun dama*
*kaci da Bismillah*
*kaci Abinda ke gabanka*
*kada kai Numfashi acikin kofi/k'waryar ruwan*
*kada kashafi band'aki da hannunka*
Ire irensu da neman yafiya yayinda kaima mutum badedaiba. Duk takoyardasu.

Bayan sungama cin Abincin, aka hau labarai anan taji labarin Uncle mai zane daduk yadda sukai dashi. Taita dariya kuwa, toilet tanufa dan haramar Sallar Magriba.

Sulaiman tunaninsu duk ya addabi kwanya da zuciyarsa, ranar da wuri yashige d'aki bayan yaci Abinci. _Recording_ na surutunsu  dayayi yazame masa abokin hira alokacin, tunani yai tayi koyaje yakaimusu  kayan gida? To maizaice, gurinwa yazo? Tambayoyin dasuka dami zuciyarsa kenan.

Cikin lokaci k'ank'ani yabi yatakura kansa, zaman hira dasuke da Umman tasu yarage, bashida aiki se saurara _Recording_ insu kusan ya haddaceshi har zanasu yai yadda yagansu. Yakumayi wani haddashi. Yaita kallan zanen hoton.

Ummantasu ganin haka tafara mai zancen yai Aure koya samu nasa Iyalin. Secemata yai

"Lokaci nayi zaiyi tacigaba damasa Addu'a.

© *Aneesa_didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: *♡DUTSEN CIKIN RUWA.....♡*
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*91*

~~~K'arshe shawarar da Umman tabashi, yaje yakai musu kayan, koya samu ganinsu yaji sassauci da rangwame.
Number wayar daya rik'eta akansa kamar karatu, wadda baisan tak'amaimai tawaye cikin wanda suka lissafo maiba, ya rubutata cikin tasa wayar. Yai jimm, yakira koya je harcan gidan? To inyaje, yace gurinwa yazo? Cin biyun dole yai d'aya. Kiran wayar yashiga yi.

Naja'atu zaune akan k'aramin cushing, Hafsa k'awarta data kamata ziyara tana mata Oiling agashinta,mai tsayi da santsi, Husna nagefanta tana bacci. Hassan kuwa wasansa yaketayi, dan intana gida duk inda tasa k'afa suna gurin. Intatafi School kuma suna gurin Inna, harta dawo.
Wayarta tashiga ruri, ganin bak'uwar Lamba harta katse bata d'agaba, yakuma kira har sau uku, akaro nahud'u ne Hafsa tadubeta tace "Haba my K'awa ki amsa mana, inkuma kink'i ni mik'on wayar nad'aga, wayasan ko sabon Miji muka samu".
Naja'atu dai batace komai ba tad'aga wayar.
"Peac be upon you, danAllah ahad'ani da friends ina, Hassan da Husna. Inason jin lafiyarsu, nakasa sukuni, since the time i was meet them, am feeling like they are my Kids". Yashiru yaji maizata ce.
Itakuwa _Husky Voice_ insa taji amonta har tsakar kanta, kalamansa nak'arshe sun ta6a zuciyarta, basan sanda tace "Kaine Uncle mai Zane da ake tamun surutunta?"
Murmusawa yai kamar yana gabanta yace.
"Nine Arc Sulaiman T Kazaure, Uncle mai Zane,i hope bazaki hanani jin muryar Yaranaba?"
"Gasu"
Tace tamik'awa Hassan wayar. "Hassan ga Uncle mai Zane".
Da murnarsa yakar6i wayar suka hau surutu kuwa hartaji yafad'a masa "Husna tayi Bacci".
Labari Naja'atu suka shiga itada Hafsat, dukda tunaninta yatafi gurin wayar da Hassan suke.
Hassan yamik'o mata wayar tasa akunnanta.
"Please Mamynmu abani Permision nazo naga yarana?"
Dariya tai tace
"Anbaka"
Batasan miyasaba tun kafin suhad'u taji yakwwanta mata, kodan yanasan 'ya'yantane.
Sallama sukai duk sun murmushi, suka aje wayar.
~~~

Yammacin ranar kuwa, segashi yazo dukda bata fito ba, yaji dad'in ganin yaran dayazo sabidasu.
Sukai tasurutu yana biye musu harda hotuna. Kayayyakin daya siya musu suka bari yabasu, hadda k'arin zanensu dayai Manya, sukad'ai dawanda yahad'a harshi. Seda yaga shigewarsu gidan shima yatafi.

Kayan suke ta duddubawa, idanuwanta sukai tozali da kyakyawan bahaushe d'an mutan Kazaure, kan Zanen dayai musu, Hoton taji yashi Zuciyarta, taita shafar fuskarsu.

Duk abinda take da yanayin datashiga, a idan Inna, Murmushi tai irin nasu na manya, zataga iya gudun ruwansu duka.

Yawan wayar dasukeyi da sulaiman, yafakaice dayiwa Hassan da Husan waya. Abin yashigesu sosai, har takai ga in ba ai wayar ba basa jin dad'i, banda sak'onni dasuke turawa junansu. dukda basu had'u ba. *Soyayya da Shak'uwa*(littafin my xoxo) tashiga Zuk'atansu.
Naja'atu gani take sabida yanasan 'Ya'yanta, shima yasamu gurbi aZuciyarta.

Sungama waya da Yaran dadaddare, yace
"Subawa Mamynsu"
Mik'a mata wayar sukai, sukatafi kallan Cartoon da Deedat yakunna.
Cikin wata iriyar murya dabata sabajin yayi irintaba a shagwa6ance yace.
"Mamyta!"
Har cikin jikinta da kanta taji amon furucin, kamar shikad'ai yafi kowa iya Ambatar sunan.
Akasalance ta amsa da "Na'am Uncle yaukuma nima nazama taka?"
Kamar yana ganinta yai murmushi tareda fad'in "Zanso hakan Mamyta"
Rintse idanu tai, besam yadda kalamun ambaton sunanta da yake lugwigwita Tanderun zuciyartaba, daya tausaya yak'i ambaton sunan.
Yakuma cewa
"Please kibani dama nanuna miki hakan, bakida matsala dani, in short kiji labarina. Yad'an gaya mata ```Biographynsa```," yakashe wayar yabatta da tunani.

Nannauyar ajiyar zuciya tayi tasan za'ai haka dama.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: *♡DUTSEN CIKIN RUWA.....♡*
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*92-93*

~~~Bata 6oyewa Inna komai akan saba, yadda yagayamata, Innartamusu fatan alkairy da za6in Ubangiji.

To 6angaren Sulaiman yagayawa Ummansa yasamu Mata, amma Bazawarace hadda 'Ya'ya biyu, Umman tai shiru kamar bazatai maganaba.
"To amma ita yarinyar tana sanka?"
Murmushi yai yace
"Batada matsala Ummana ki amince tazama Surukarki, Matar d'anki, dazata bawa Autanki cikakkiyar kulawa."
Umman tadubeshi tareda cewa "to Allah yatabbatar da Alkairi."
Rungumeta yai yace "ina sanki Ummana, Nagode Nagode yabata peack agoshi."

Dariya Umman tahauyi, tana hango yadda Matar dazata Auri Sulaimanunta zatai d'awainiya dashi, da shagwa6a dukda ya girma befasaba.
Sukaita hirarrakinsu kafin akirashi awaya yafice daga Gidan.

Fad'uwar da gabanta yake ya tsananta aranar, tunda Sulaiman(Uncle mai Zane) yace mata zaizo.
Simple makeup tayi, ita kanta kwalliyarma takwan biyu bataiba. Less _Mint Blue_ tasa riga da skirt tai d'aurinta daidai da zamani, spray tasa kad'an da turarenta _Urban Woman_ ta d'ora babban gyale akan kayan. Jelolinta Hassan da Husna suna gefanta suma sunsha ado. Sun nutsu kamar basuba kar ace kartace bazata fita dasuba. Ta dubesu tai murmushi.

Wayarta tashiga Sauti, Hassan dasaurinsa ya mik'a mata, ganin sunan "Uncle Sman" a Screen d'in wayarta, dan haka tai _saving_. Samun kanta tai  da rikicewa kaman bata ta6a tsayawa da namijiba. Seda takai zuciyarta nesa tad'aga wayar. Cikin sassanyar muryatta, ya amsa tareda langa6ar dakai "Ran Gimbiya yadad'e, fatan nasameku lafiya?"yafad'a kamar yana gabanta.
Murmushi takumayi, suka gaisa yasanarmata dagashi ya iso, tasa aimasa iso. Seda tai jim sannan takashe wayan.

Innarsu tasanarwa take tasa Fawad yashigo dashi falon bak'i na Babansu, Ruwa tabayar aka kaimasa da leman d'anyar citta, daya d'au sanyi dai-dai sha had'eda Meat-pie.
Akunyace tacewa Inna bari taje, tabita da Murmushi tanaimata Addu'ar samun Alkairy.

Zaune yake d'aya daka cikin Kujerun falon, wadda take fuskantar k'ofar shigowa, yanata danna wayarsa. Sassanya kuma Zazzak'ar Muryatta datai masa Sallama tasashi d'agowa, ya amsa idanunsa akanta, sanda ta d'ago itama idanunsu suka had'u, dukkansu saida wani bak'on al'amari ya tsirga musu, itatai saurin d'auke idanunta ta sunkuyar dakanta.

Tana guri guda daka can gefe tazauna, su Hassan da Husna suka gaidashi kowa ya mak'ale agefan kafafun "Uncle mai Zane" injisu da fad'a.
Naja'atuma ta d'ago kai tareda rusunawa tagaidashi "Barka da Yamma" muryatta kaman ana busa sarewa.
~~~

Ya maidamata da "Barka kadai Mai kyau, nasameku Ipy?"
Murmushi tai daya k'ara fito da tsantsar kyanta. Tace "Lafiya lau ya mutan gida?"

Hira yaitamata, dukda rabin hira ta Yarantace, Hassan da Husna, sedai tad'an saki jiki dashi kad'an.
Jaka yad'auko agefansa guda biyu, yabasu kowa d'aya ahannunsa yace "Sukaiwa Inna" danduk yaji labarinsu gurin 'yan biyu, yahad'asu da Sweat suka fita sunata Farinciki. Dukkansu suka bisuda kallo suna murmushi.

Haske tagani Walll! Tajuya tana kallansa, yasakar mata k'ayataccen Murmushinsa daba kowa yakewa shiba. Waya tagani a hannunsa alamun Hoto yamata. Sulaiman Ganindayai takafeshi da _Bold Eyes_ d'inta yasashi cewa "Am sory  Ummana zan kaiwa taga Surukarta mai kyau that why nai Snapinng naki dukda Original Pic inki yananan Album guda a Bottom of my heart" sunkuyar dakai takumayi ganin irin kallon dayake binta dashi yace "Lallai yau kinaso nakwana gidannan indai zaki cigaba damun wannam Smile innaki dake tafiya da Ruhin mai kallo, Uwa Uba Kunyar ki datake k'aramin shauk'in san kasancewa tare dake."

Anan yarik'a bayyana mata *Babban Sirri (My Yaya Hajja Novel)* dake ransa. Ita kuwa Naja'atu mamakinsa take daga *Had'uwar Farko* mutum ya zak'e, lallai saitayi dagaske zata gano irin San dayake mata bata k'ara mamakantuwaba seda taji Sulaiman yace "Naja'atu ga k'ask'antaccen bawa yazo gareki da k'ok'on barar soyayya har tazama ta Aure *Ni dake (Phertylicious ta)* muzama k'ark'ashin inuwa d'aya, ga miji yazo gareki akaro nabiyu. Amma zanbaki lokaci ki shawara saidai da had'uwarmu da Auren  bazai wuce wata biyuba banma son hakan."
Baijira maizata ceba yaimata sallama yatafi.
Ita kuwa Naja'atu bin bayansa tai da idanu harya fice. Dak'yar tatattaro dukkanin nutsuwarta tashige cikin gida.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: *♡DUTSEN CIKIN RUWA.....♡*
*Na*
*Haleema  G Khaleel*

*94-95*

~~~Lokutan dasuka biyo baya, duk batada sukuni. Gani tai Tunanin bazeje mataba sai tashiga adduoi da neman za6in Allah.
Har d'an fad'awa tayi yasa Inna takuma mata nasiha.

Kullum cikin dare zatai Nafila Raka'a biyu ta *Salatul Istikara* tai addu'a danneman za6in Ubangiji.
~~~

_Garemu 'yan uwa Musulmi yayinda wani abu yashige mana duhu komike shiga dabaibayi gameda neman abu ko samun abu na Rayuwa, Neman Aiki, Neman Aure, Karatu. Wani Abu dai makamancin haka. Inmukai hak'uri komi mai sauk'i ne_.

Cikin Hisnul Muslim(Garkuwar Musulmi) dasauran Litattafai na Addini da Addu'ar tazo.

*Jabir bin Abdullah Allah yak'ara musu yarda: Manzan Allah S.A.W yakoyar damu ISTIKHARA acikin kowane al'amari kamar yadda yakoyar damu sura daga Al-Qur'ani yana cewa:- "Idan d'ayanku yana dawani Al-amari seya Sallaci Sallah raka'a biyu, badaga cikin Farilla ba, seyace:-* ```ALLAHUMMA INNI ASTAKIRUKA BI ILMIKA, WA'ASTAQ DIRUKA BIQUDRATIKA, WA'ASALUKA MIN FADHLIKAL AZEEM. FA'INNAKA TAQDIRU WALA AQDIRU, WATA'ALAM WALA A'ALAM, WA ANTA ALLAMUL GUYUB.
ALLAHUMMA INKUNTA TA'ALAMU ANNA HAZAL AMRA(ka/ki fad'o Matsalan taki ko wani abu daki/ka ke nema) KAIRULLI FI DINIY WA MA'ASHI WA'AQIBATA AMRI, FAQADIRHULI WAYASSARHULI SUMMA BARIKLIY FIHI, WA INKUNTA TA'ALAMU ANNA HAZAL AMRA (ki/ka fad'o matsalan kowani abu daki/ka nema) SHARRILY FI DINIY WAMA ASHI, WA AQIBATU AMRI FASRIFHU ANNIY WASRIFNIY ANHU, WAQADURHULI KAIRA HAISU KANA SUMMA ARDINIY BIHI.```
Yaitayi in sha Allahu zaisamu daidaito da za6in ubangiji.

**********

Sulaiman kuwa, Mahaifinsa yasanarwa yasamu mata danhaka Addu'ar dasuke masa akullum lokacinta yayi, sai aje anemomasa Auren.
Ba jimawa Manya suka shiga maganar, aka tsaida za'a d'aura musu Aure tareda 'yan uwanta inyaso tatare daga baya.

Shirye-Shiryen biki ake tayi. Amaren Gidan se kintsasu ake da gyata according to Sunna.
Wayar da Sulaiman kemata, sema abinda yak'aru, har fad'a sukeyi yadda tak'i sakin jiki suzuba Soyayya dashi. 'Yan biyunta su Hassan da Husna sun zama 'yan Gidansu "Uncle mai zane" bawanda besan dazamansuba se yayunsa dabasanan kokuma insunzo lokacin bekasuba. Yazama wani sashe narayuwar yaran dayalashe gurbi dadama a zuk'atan yaran da 'yan uwan Naja'atunma tukafin ya Auri Mahaifiyarsu. Hakan yasa duk yasamu Shaidun k'warai dakykkyawan zato.

Agajiye liss! Tadawo gida daka Sch karatun yad'auko k'arewa basuda wani hutu inba _Exams_ dake gabansu sukai suka gamaba. Ga abubuwa duk sun had'e mata, wayanma ba kasafai take barinta akunneba.
Ruwa tawatsa tazauna tana hutawa, dan fashin Sallah take alokacin. Riga ce Bubu me fad'i ajikinta me launin ruwan Madara tasaka hula ruwan k'asa se k'amshin turarenta na _Urban Woman_ take. Wayarta takuna bata jimaba kiran "Uncle Sman" yashigo kamar bazata d'agaba.
Jin sassanyar muryatta yasashi sakin wata wahalalliyar ajiyar zuciya yace "Haba Mamynmu(inyaso raha haka yake kiranta dashi) kina wahal da daddyn yarafa, ko laifi nayi

bansaniba?"
"Ah ah fa Uncle"
"To miyafaru?"
"Allah Uncle ina busy ne dayawa kasan munkusa fara _Final Exams_ dole wasu abun semun hak'ura dashi mi _Concentrate_ akaratunmu kodan muwuce gurin kawai."
Tafad"a dawata irin Murya a shagwa6e.
Numfashi Sulaiman yakuma saki yace
"Allah sarki kice inzo miyi karatun tare, bakomi ma ai nasan Mamynmu _Gifted_ ce ko _Guru_ zance?".
Dariya tasaki tana "kaikam kacika tsokana. Nidai katayani Addu'a kawai."
Irin muryatta yakwaikwaya yabata amsa. Dariya takuma saki sukai ta hira kamar karsu rabu.

Abinda yai shirin fad'a mata ma yabarshi ganin abubuwane agabanta ba kad'an ba.
"Ina sanki Naja'atu"
"Hmmmmmm! Alamun ajiyar zuciya yaji. "Nibazakice kina sonaba?"

"Ina sanka mana Uncle, kaine sanyin idaniyata dazaka maye gurbin abubuwa dayawa... harda zuciya...." bata k'arasa fad'in maizatace ba da _Hanging_ wayar ganin shigowar Inna dasu Ibrahim da Isma'il Yayunta, wanda alokacin sunzama matasa sosai dako Auren kowace mace sukaje nema za abasu yadda Allah yaimusu kwarjini da Baiwar kyau tsantsa. Sunkuyar dakai tayi tana juya Cup in hannunta. Ganin basuce mata komaiba, taware sukaita hira wadda yawancinta ta bikin dazasine da yadda suke shirya Al-amuran sukasance cikin lafiya da kwanciyar hankali har agama bikin.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*96-97*

~~~Da ikon Allah, aka fara shagulgulan biki. Hausawa sukace Rana bata k'arya.....!
Asabar 12 gawatan Goma dubban jama'a suka shaida d'aurin Auren 'ya'ya hud'u na Alh Abdul-Muiz Auwal, Namiji d'aya da Mata Uku. D'aurin Auren yaya Hafiz akafara d'aurowa Tudun maliki, da Amaryassa Maryam.
Juwairiyya da Angonta Aminu. Samiha da Mukhtar, wanda silar had'uwarsu Allah yamasa shiriya kamar dawasa suka fara Soyayya da Samiha kuma Allah yai matarshice takaisu gayin Aure ayau.
Akaro nabiyu aka kuma d'aurawa Naja'atu Aure da Angonta Arc Sulaiman Kazaurw.

Yana daka cikin Al-adun bahaushe nawannan lokacin yayin Aure. Bayan and'aura Aure,
~~~

Angwaye da abokananansu, sukan shiga gidansu Amarya domin gaisawa da Iyaye Maza da Mata. Hakance takasance gidan Alh Abdul-Muiz A yacika fal da Jama'a masu Hotuna, da Marok'a seyi suke.
 Mazajen Samiha da Juwairyya se hotuna ake musu haka Yaya Hafiz ma anatayi dawasu 'yan uwan. Sa6anin Sulaiman dayakasa ganin tasa Amaryar se washe baki yake kaman gonon Auduga. Abokansa kam se tsiya suke masa.

 "Yanzuke hakan dakike yayi dai-dai kenan? Inma bazaki shiruba yaci kin kammala shiryawa" Inna data shigo tatsaya akan Naja'atu datake ta shar6an kuka, tunda akakusa bikin tazama sukuku da ita duk tasusuce banda ramar data kumayi. Dayawa sunmata magana tak'i shiru sega Innartasu takuma dawowa.
 Anty Husna ganin datai kamar Inna zata rufe Naja'atu da duka tai saurin matsawa kusada ita, Lalla6ata tashigayi ahankali tana mata Nasiha "Haba Daughter na kedama bayau ko gobe zaki tafi gidan mijinba. Ko Samiha kiduba daza akaita gobe batai wannan kukanba ammake anrasa Kukan mekike ko Aurenne bakyaso?" Tana kallanta ta girgirza kai "To maza kishiru kinji Aure ai Ni'ima ne da Daraja. Shine Cikar Zati Kamala da Mutuncin duk wata 'YA MACE muddin tarik'e mutuncinta tobamai kyetamataahi. Kuma kowace Uwa dakikagani Burinta ta Aurar da 'YA'YA MATAn dake gabanta shine samun nutsuwa da kwanciyar hankalinta. Kowa kuma da haka tasaba. Maza k'arasa shiryawa kar Mijinnaki yazo yaganki haka, kinji 'yar albarka". Shiru tai duk tasaurari metace k'awarta Jidda da Mino dake fama da ciki sukai tamata iya-ege, ahaka suka k'arasa gyaramata kwalliyarta data 6ata da kuka suka Shirya fes da french less coffee colour damayafi milk&coffee har kanta se k'amshi take Amarya tafito fess da ita se ajiyar zuciya datake saki.

 Gud'ar dasuka jiyoce, taji wata mata dabata gane waceba tanata Kabbara, sekirari takewa Inna da 'Ya'yanta. Sulaiman suka shigo har falon Inna gaisawa sukai tayi da 'yan uwa dake falon. Anty Husna tajata suka fito falon, kanta asunkuye. K'walla tataru a idanunta. Masu hoto da masu d'auka da waya sukai tayi hasken Flash kawai kake gami.

 Kukan datake 6oyewa ahankali take shashshek'a, Sulaiman datun shigowarsu seda yaganta farincikinsa yak'aru. Bayan mutane sund'an ragu a falon, duk'addakai Sulaiman yai yad'an tallafo Naja'atun sesuka bada wani Style masu Cemara kam mezasiyi ba hotoba akaita _Snaping_ insu. Ni Aneesa_Didi Duk k'ok'arina na injiyo muku meya cemata akunnenta banjiyoba murmushi nikaina nasa ganin kowa yana darawa.
 Itakam ganin Sulaiman naneman bata kunya yasata sakin murmushi tareda janyewa daka jikinsa nikuwa nace kaga Masoya. _Gud Moment_ kenan "Tears & Smile".

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:50 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
*Haleema G Khaleel*

*98-99*

~~~Haka akai biki aka gama cikin farin ciki da Annushuwa, su Husna da Hassan shigar sababbin kaya akai tamusu. Yara masu kyau dashiga rai, kowa sansu yake duk inda suka shiga kamar kasace kagudu abin gwanin ban sha'awa.
Inna nasa k'afa suma suna sauke tasu ko ina suna biye da ita sabida Mamynsu Hauahin kowa takeji jin ance "bazata tafidasuba kosu koma gidan Kakanninsu, duk dashi a 6angarensa bashida matsala Sulaiman ya amince zai Rik'esu koba komai Rik'on Maraya Ladane kuma D'A NAKOWANE. Amma iyaye sunce sesun duba labarin. Hakan yasata 6acin rai.

Sharar hawaye take akai-akai yaranma ko kallansu batayi.
Washegarin ranar lahadi. Daga cikin yayunsu mata Anty Husna ma tabi wanda zasu gidan Samiha suka tafi gidan Amaren dan k'ara gyagygyarawa kafin akai Amaren.

K'arfe uku na yamma agogon Nigeria Niger da Chad. Shirye shiryen kai Amare Juwairiyya da Samiha ake ana la'asar za akai kowacce gidan Mijinta.

Inna dai bata tankaba ganin ita Naja'atu se shirye, shiryen fita take da alama 'yan kai amarya zatabi. K'anwar Babansu Gwagwgwo ta Getso tashigo ganin Naja'atu tana fesa Turare yasata cewa "Hala kai Amarya zaki kema?" Sunkuyar dakai tayi "Ah Gwaggwo dan Allah kuje dani" cike da shagwa6a tai maganar hadda langa6ar dakai.
Dariya sukayi 'yan d'akin. Gwagwgon takuma fad'in "Ai tafiya dake babu matsala mutuk'ar dayaddar Mijinki maizai hana mutafi dake, tunda ke tariyar ba yanzuba." Ai jitai kamar tasa ihu! Matar wansu dasuke mutunci da ita tace "Maida wuk'ar yanzu da Aure akanki, inda zaki fita dole saida izinin ma'ana kin tambaya komai kinma sani ai, sedai k'arin bayani. Ki kirashi kisanarmai inya amince muje mudawo ko Gwaggwo?".

Naja tai shiru tamkar bazatai maganaba. Ganin anata shirin tafiya kai amaren har anshiryasu ankaisu gurin Baban dasauran Matan Gidan sekuka suke. Yatsuna fiska tai kamar tahak'ura ma dazuwa, tai tunani to aikuma batada ranar zuwa k'ara taje yanzu ayama.
Kiran layinsa tayi seda tai Ringin Hud'u yad'aga "Ran Gimbiyata kuma Amaryata yadad'e!" Rasa maizatace tayi dabara tafad'o mata tace "Tare dakai fatan kana lafiya?"
"Alhandulillah, muna lafiya dani har Matata dakowama."
"Uncle mai Zane"
"Na'am Mamyn uncle mai zane"
Shiru bawanda yakuma magana sai numfashinsu dake shiga kunnuwan junansu.
"Dama wai zanbisu kai Amarya shine wai Gwaggwo tace sena tambayeka" tafad'a harda cuno baki kamar anmata dole.

Dariya Sulaiman yai sosai lallai Matar tasa 'yar daruce ko rigima zaice. Jin yana dariya taji inama bata kiraba, kamar takashe wayan taji sedai koma takashe abanza kiranta zaikumayi.
~~~

Taji yace "Tajirashi yazo yakaita dakansa danba mai kallrmasa kayansa"
"Haba Uncle ga Jama'anan muna zuwa zamu dawo damafa Gwaggwo zamu."
Duk yadda tabi k'iyayi dole shid'in yazo yakaisu. Samiha ita banisa cikin Unguwarsune. Juwairiyya itakuma aka kaita Hausawa.

Semuce Allah bada zaman lafiy da k'azantar d'aki amma bata sharaba.

Exams in su Naja tazo shikansa Angonnata Sulaiman sarara mata yai dayin Waya. Dantasamu tai karatun final Exams inta. Dataimakon Allah suka kammala exam inau da makarantarma duka sejiran sakamako.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
[2/18, 10:52 AM] +234 703 962 5239: ♡ *DUTSEN CIKIN RUWA.....*♡
*Na*
® *Haleema G Khaleel*

10 jan 2017

*100*
🔚

*_But if they intend to deceive you. Then sufficient for you is ALLAH. It is he who Supported you with his help and with the believers._*

~~~Tunda tafara exams Sulaiman ke kaita yadawo da ita harta kammala.
Watarana yad'aukota daka sch suntsaya a _Go slow_ a junction mutane se hada-hada, suke. Un expected taji anrik'o hannunta abinda Sulaiman beta6a mataba, dagashi har ita wani _Haptonasty Reaction_ sukaji sosai yakuma rik'o hannunta ganin abinnasa nakuma k'aruwa cike da shagwa6a ta turo baki "Allah kaban tsoro kuma sena rama" dariya sosai tabashi yadda bakinta ke motsi da shagwa6anta ya birgeshi yace "to ai nariga nabiya dan wannan kawai, barikiga kad'an daka ciki..." Gaba d'aya ya janyota jikinsa yafara Sumbatar bakinta cikin nutsuwa k'amashin Air freshner motar da Turarensu suka had'u suka bada wani Sanyayyan k'amshi mai Sanyaya zuk'ata. Hakan yakuma ingizashi yakuma rik'ota tako ina aikamata zazzafan sak'o yake yanakuma shafota.

K'arar horn d'in da ake yimusu yayi yawa, dole yahak'ura. Saurin komawa mazaininta  Naja tayi d'ankwalinta dayazame tagyara had'eda mayafinta. Allah yasa Motar da Tinted, nawaje bazega nacikiba amma naciki naganin nawaje.
~~~

Sunkuyar dakai tai tana wasa da abin mayafinta, tafiya suka cigaba dayi. Jefi-jefi yana dubanta yana sakin wani k'ayataccen murmushi dake k'aramasa kyau da kwarjini.

Sunkusa kaiwa gidansu Naja'atu yai Parking dai-dai gurin wasu masu nama wanda anan suke siyan Nama kowane iri kakeso zakasamu agurin "Haleema Suya Spot" fita yai daga motan yace "yana zuwa."

Binsa tai da idanu aranta tana tunanin dama haka Sulaima  yake shima d'an soyayyane, murmushi tai tana kuma tuna abinda yawakana mintina kad'an dasuka wuce.

Bedad'eba yadawo da ledoji a hannunsa. D'aya yasa abayan motar, leda biyun kuma ya d'oramata akan cinya yad'ora dacewa "Ga Tsiran Tsira da Soyayyanan da Kilish, dukda ni nasan tawa a Safe content take."

"Kai Uncle wannan Confidence haka"

Dariya sukai duka yaja motar yak'arasa da ita gida sukai sallama yawuce dan cigaba da shirin taryan Amaryassa.

Kwana biyu da gama Exam inta, Babansu yasa dole tatare asatin fad'a sosai yamata. Hassan da Husna karma susata kuka aka kaisu gidan kakanninsu. Maman aranta taso datana dawani babban d'a Namiji ya auri Naja'atun takasance cikinsu. Yanzuma addua da fatan Alkairy suka mata. Daga canma gidan Yaya Yusra aka kaisu yar Usman Mahaifinsu.

Ranar Jumu'a k'arfe Hudu da rabi, kamar yadda akakai sauran 'yan uwanta. 'Yan uwa da abokan arzuk'a nakusa suka rakata gidan Mijinta akaro nabiyu dake d'an Agundi G.R.A. kuzo kuga wani _Mension_ da Arch Sulaiman yazana Tasweerar Gidan dakansa. Tundaga wajen gidan abin kallone, ido nabud'e harda hanci da baki ina kallon Aljannar duniya.

Varender ce dazata sadaka da Falo mai Girma d'auke da Kitchen, Dining Area Toilet sewani D'aki da toilet ahad'e. Daga gefe nagano Stairs dabasu dayawa duk cikin falon zubin ginin Indiawa. Inka haura Saman d'akunane manya guda uku da aka k'awatasu kowanne d'auke da Toilet aciki launi daban-daban se Varender tasama itama.

Gidan gaba d'aya abin kallone 'yan kai amarya se san barka suke dasa albarka. Amaryan nagano cikin wata Gown zubin Qatar anrufeta sinkif se walainiya take da tashin k'amashi. Wani _Purple bedroom_ aka ajeta akan gadon da Fulalluka suka yawaita akai. Nikaina nadad'e ina santin d'aki (Lol).

Kafin Maghriba kowa yatafi akabrta se wasu daga cikin dangin Sulaiman, kukan dataitayi hartagaji tabari har ango  yazo yasameta. Nafila suka gabatar tareda 'yan Tand'e-tand'e da lashe-lashe Nakaji da lemuka harda Tsiran Tsira da Soyayya, nima Uncle mai Zane yaban K'unshi d'aya yace nasanwa Miss xoxo da besty miss Fais ceeda, danyaga abimnamu iri d'ayane.

Tsayawa nai abakin k'ofa gan Sulaiman yafara Rud'a Naja'atu da sak'on Soyayyarsa mai girma, fuskarsa yake kuma cusawa jikinta yana k'ok'arin rabata da kayan jikinta azafafe yake shafarta har tausayi sukaban, se numfashi suke saukewa suka Lula Kogin Soyayya mai Sanyi da Wahalar Nink'aya. Bashiri nai waje. Tsiran Tsira da soyayyan da akabam nawarware nafara ci. Kuma Makaranta ganaku. Hhhhhh.

************

BAYAN WASU LOKUTA

~~~Soyayya suke gwadawa Junansu mai tsafta. Dukda ZAMAN TARE zomu zaunane zomu sa6a. Yaransu masu kyau. Namiji tafara haifa maisuna Sufyan, Zuwa lokacin Hassan da Husna sunk'ara girm. Babu tayadda zakace ba 'yan gida bane, kowa sansu yake adangin Sulaima. Suntaso da soyayyar dangi da gata.

Haihuwar Safiyya takumayi 'yar Babynta gwanin sha'awa mai gashi da ita ba inda tabaro Umman Sulaiman.
Zama suke maitarin Aminci K'auna da Soyayya dakuma Hak'uri da Juriya akomi na Rayuwa dayasamesu medad'i ko akasin haka.

Girki tagama takuma salla wanka wata Fitted Riga da Zani tasa na Atamfar Vilisco launin sky blue da maroon ahad'e tasha _Makeup_ sek'amshi take takuma cika sabida jegon datake 'yar Chafai da ita. Bazakace tayi yara Hud'u ba. Hutawa take ita kad'ai se Baby Safiyya(yadda su Hassan ke gayamata) sauran yaran duk taturasu gurin Umman, tagyare gidan dataimakon Sulaimam kafin sufita. K'amshin turaren data sa a electric burner ketashi cikin gidan. Safiyyan tana kan jikinta anmata gayu itama tasha hoda b'angala dariya take, dahaka tasamu talalla6ata tai bacci. Kusada ita takwantar da ita.
Wani Novel take karantawa maisuna JANAN na (CHUCHUNA AYEESH) sallamar Maul'ainain(Ruwan idonta) taji Sulaiman nagano yakuma girma, Sumar kanashi se k'yalli take gawani Zagayayyen gemu daya ajiye wanda yakuma k'awata fuskar tashi da 'yan mata kerubibi, basusan Naja takafa ta tsare kuma taraka.

Sama da ita yai sukaita zagaye falo sannan yadireta. Tabaya yarungumota tsam har tanajin bugun zuciyarsa. Farar takadda yafito da ita yace tarik'e, akunne yarad'a mata "nagode Allah matata mai sa'ace gashinan and'aukeki aiki a General Hospital, so get ready nanda 1-2month zaki fara attend" wani juyi tai takuma rungumo mijinnata "Alhamdulillah Nureena, Wht a Suprise Habibi" nagode sosai mijina na har abada hak'ik'a KAINE GATANA kuma FARIN CIKINA. Allah yabiyaka da d'umbin alkairy yafarantama ka kamar yadda kakemana. Nakuma Godewa Allah yadda mukazama DUTSEN CIKIN RUWA DABAI SAN ANA RANA BA. Dagamu har Mahaifiyarmu tayi hak'uri muma tad'oramu akai. Tabbas Hak'uri Ribar Rayuwane. Ba irin nacin dabanyiba kabarni nai Aikin kak'i yanzu kaga nasamu amincewarka 100% nagode Allah dasamun miji irinka. In sha Allah zanyi aiki sabida Allah zantaimakawa Al umar musulmi kuma zankare DARAJA DA MARTABAR AURENA. Allah yak'aramana lafiya dazama Lafiya.

_Deep french kiss_ tashiga aikamasa sak'on kuwa yashigeshi yafara fita hayyacinsa yana ba Amsa danasa salon Sak'onnin. Cak yad'auketa sukai samansu d'aki sukai tareda rufo k'ofa. Dole najuyo nace asha soyayya lafiya.
~~~

_Soyayya gaskiyace Allah yabarmu da masoyanmu ako ina suke_

Alhamdulillah!!!

Anan nakawo k'arshen wannan labari. Kurakuran ciki Allah kayafemana kazama jigonmu.

*$adarkrwa garekune*
Hafsat GL (Miss xoxo)
Masoyiwa kuma 'yar uwa
Aneesa A Rimi (Mamyn swty Ayman)

Haleematu Bukar Saje
Kinfi kowa san littafinnan. Allah yabar k'auna da zuminci.

'Yan uwa marubuta inamuku fatan alkairy. Allah bar zuminci.

Duk wanda ya isa gareshi nagode sosai da tarin sak'onne da soyayyarku. Inbabu ku babumu. Allah yahad'amu da rahmarsa.
K'arshe.
Semun had'u asabon labari.......
Taku maik'aunarku
Haleema Sadiya g Khaleel.

© *Aneesa_Didi*🍼🍉😜
Copied By
HAYATU BABA ZUBAIRU
(admin
Arewa hausa novels
Novels villa
Duniyan novels
Hayat hausa novels
Hausa novels and fashion
And
Cool novel, makeup and cooking)

WHATSAPP NO:
+2347039625239